

# SHIRIN ALLAH DOMIN ALMAJIRANTAD DA MATASA



Shirin Allah Domin Almajirantad da Matasa zai zama kwakkwaran harsashi ci gaba da zai taimake Matasa su fara rayuwa ruhaniyamai kyau

## LITTAFI NA ALMAJIRANTAD DA MATASA

# Shirin Allah Domin Almajirantad Da Matasa



# SHIRIN ALLAH DOMIN ALMAJIRANTAD DA MATASA

## Littafi Na Aiki Na Almajirai Matasa

Wannan littafi na aiki da yara da matasa tare da darisai, ayyukan yi da yawa da abin koyi ga matasa a kowane zamani. Manufar wanna littafin aikin domin ya inganta da karfafa matasa mabiyan Kristi a girman su na ruhaniya da amfani da ka'idodin Littafi Mai Tsarki wanda al'ada da lokaci ba su sa mata iyaka ba.

Tim W. Bunn da Virginia J. Dickens.

**Bugu na Daya, 2021**

Copyright© 2021 by New Foundations International

# Shirin Allah domin Almajirantad da Matasa

## Littafi Na Aiki Na Almajirai Matasa

Scripture taken from the International Children's Bible®. Copyright© 1986, 1988, 1999 by Thomas Nelson. Used by permission. All rights reserved.

ISBN: 978-0-578-86396-2

Book front Cover:

**Alford Usher Soord (1868-1915) da firinta ne daga Birtaniya, wandda sanannen aikin sa ita ce bugun Misalin Batacen Tunkiya wadda ta nuna dan tunkiya da ta makale a tsakiyar gangarar dutse kuma makiyayinta na rataya mai hatsari a bakin dutsen, ya sadakar da ransa domin cetan tunkiyar. An nuna zanen Batacen Tunkiyan a shekara ta 1898 a Royal Academy kuma a shekara ta 1916, an kwaikwaiya ta har sama da 300,000. An sayar da zanen a kasar Ingila da Amurka; aikin ta cigaba da zama mashahuri ta musamman fiye da karni daya bayan halitarsa.**

**First Edition, 2021**

Copyright © 2021 by New Foundation International

New Foundations International website:

http://www.newfoundationsinternational.org/

Please contact us or send a request for information on:

**nfi@newfoundationsinternational.org**

# SHAIDA

Karfafa don rubuta wannan littafi ya zo ne daga koyarwa iyaye a Amirka ta Tsakiya akan shirin Allah domin ya'ya Almajiransa.  Godiya ga Martha Dickens Evans domin taimako da abinda koyarwan ya kumsa.  Muna so mu nuna shaidar godiya ga Danielle Nash, wanda ya taimaka da zane-zane (graphics) cikin sauki domin yara su yi launi da kuma su tuna gaskiyar Littafi Mai Tsarki tare da darisai da ke ciki.  Haka ma muna gode wa Sherman Driver domin karfafawa da taimakon cikin daidaita wannan aikin (project) zuwa littafin aiki mai amfani.

# GABATARWA

Wannan shine kwakwaran harsashin kayan aiki da aka shimfida da taimakon ka ci gaba a ruhaniya mai kyau farawa daga nan da kai cikin maganar Allah, Littafi Mai Tsarki, Tawurin hotuna, labarai da aikace-aikace.

## Kafin Ka fara:


Kafin ka fara wannan nazari na shirin Allah domin Almajirantad da Matasa, yana da muhimmanci cewa ka amince Yesu Almasihu ya gafarta zunubanka da marmarinka na bin Yesu. Kafin ka zama almajirin Almasihu, dole ka fara da gaskata shi da zama mai bin Almasihu.  Idan ba ka san Yesu da kanka da kuma karbe shi kamar Mai Ceton zunubanka ba, ko idan ba ka tabbatar ba, in ka yarda ka karanta da yi nazarin labarin da ke kasa. Mai kan, Magana **Ceto tawurin Yesu Almasihu** domin ya taimake ka daukan wannan muhimmiyar shawara.

Kana bukatar ka tambayi iyayen ka, Fasto, ko Malami ya taimake ka da tambayoyi da ka ke da shi da kuma shaida ma wandansu shawara da ka dauka.

# CETO TAWURIN YESU ALMASIHU

Kana shirin fara nazari akan yadda za ka zama almajirin Yesu Almasihu nagari. Idan ka ci gaba `cikin nazari da kuma Littafi Mai Tsarki, za ka karu sosai akan zaman mai bin Almasihu wanda ke biyaya da Allah. Wannan ya hada da zaman biyaya ga maganarsa cikin Littafi Mai Tsarki, biyaya da na gaban ka a gida, da biyaya cikin taimakon wadansu cikin iyalin Allah domin ka zama almajirai nagari.

Kafin ka zama almajirin Yesu nagari, kana bukata ka tabbata ka zama daya daga cikin masu binsa. Hoto na kasa zai taimake ka fahimtar yadda za ka zama mai bin Yesus Almasihu (dubi Shafi 8 domin Karin taimako).



Hoto a shafi da an wuce yana nuna mutum, dukanmu, a gefen hagu babu Almasihu. Kana gefen da akwai rami mai zurfi. Allah yana dayan gefen. Ka rabu da Allah domin zunubanka. Zunubai sune ababa da kana yi da baya faranta ma Allah rai. Ba abinda za ka yi da zai tamkake ka kai wurin Allah… ba zama mutum mai kyau… ba zuwa majami'a ba… ba yin ayyuka masu kyau ba… ba biyan kudi ba… ba kome. Mutuwar Yesu akan giciye domin ka kadai zai iya zama gada akan ramin zunubi mai zurfi domin ya cece ka.

Dole ka gaskata da abinda Allah ya ce cikin Littafi Mai Tsarki: cewa kai mai zunubi ne, cewa zunubinka ya raba ka da Allah, kuma ba ka iya yin kome domin ka ceci kan ka daga zunubin ka ba. Ka fadi wa Yesu kana bakin ciki da zunuban ka. Tambaye shi ya gafarta maka zunuban ka da kuma ya taimake ka ka rayu dominsa. **Bangaskiya cikin Yesu Almasihu kadai zai iya cetonka.** Tawurin jininsa da ya zub da shi kadai domin mu akan giciye za mu iya samun gafarar zunubanmu.

Idan ka rigaya ka gaskata Almasihu ya gafarta zunubanka, ka shirya ke nan ka fara koyon yadda za ka yi rayuwar mai bin Almasihu.

Idan ba ka rigaya ka gaskata Almasihu ya gafarta zunubanka ba, ***yanzu*** ne lokaci da ka tsaya ka yi haka.

- **Yi addu'a ka kuma fadi wa Allah bakin cikin zunubanka**. *"In kuwa muka bayyana zunubanmu, to, shi mai alkawari ne, mai adalci kuma, zai kuwa gafarta mana zunubanmu, ya tsarkake mu daga dukan rashin adalci"* (1 Yahaya 1:9).

- **Ka aminci cewa Almasihu kadai zai gafarta zunubanka da maida kai sabon halitta cikin Almasihu domin ka iya binsa da yin biyaya yadda Allah yana so ka yi rayuwanka.**
- 

  *"Ta gare shi ne muka sami fansa albarkacin jininsa, wato yafewar laifofinmu, bisa ga yalwan alherin Allah"* (Afisawa 1:7)

  *"Saboda haka, duk wanda yake na Almasihu sabuwar halitta ne, tsohon al'amari duk ya shude, ga shi kome ya zama sabo".* (2 Korin. 5:17)!

Za ka iya yi addu'a ka gaskata shi yanzu, ko da kai kadai ne. Idan ka yi haka, ka kuma fadi ma wani da ka sani mai bada gaskiya cikin Almasihu game da shawara da ka dauka kamar iyaye, fasto, ko malami. Ka iya roki daya daga wadannan mutane su taimake ka, idan akwai ka da tambayoyi. Muhimmin abin shi ka bada gaskiya, mai bin Almasihu. Ta haka kadai za ka yi shirin fara koyon yadda za ka zama almajiri Yesu Almasihu na gari.

**Ka gama launin giciye na ayyukan shafi na kasa domin ya taimake ka Karin gane akan ceto ta wurin Yesu Almasihu.**

# Yi Launin Giciye

Umarnai:
Yi launin **Sama** rawaya **ko** rubuta 1 cikin bulon
Yi launin **Zuciya Mai Zunubi** a bulon da bakin launi **ko** rubuta 2 cikin bulon
Yi launin **Jinin Yesu** a bulon da Jan launi **ko** rubuta 3 cikin bulon
Yi launin **Zuciya Mai Tsabta** a bulon da farin launi **ko** rubuta 4 cikin bulon.
Yi launin **Girma Cikin Almasihu** da koren launi **ko** rubuta 5 cikin bulon.



# JERIN ABUBUWA DA KE CIKI


**Shirin Allah Domin Almajirantad da Matasa – Kashi Daya 8**

I. Ikon Almajiri da isan su 10

_______Nazari 1 – Iko da Isan Maganar 10

_______Nazari 2 – Iko da Isan Ruhu 16

II. Biyayan Almajiri, zaman Memba da Tunawa 22

_______Nazari 3 – Baftisma ta Ruwa 22

_______Nazari 4 – Membobin Juna 26

_______Nazari 5 – Jibin Ubangiji 30

III. Tabbatatun Almajirai cikin Nazarin Littafi Mai Tsarki 34

_______Nazari 6 – Umurnai a yadda za a yi Nazarin Littafi Mai Tsarki 34

_______Nazari 7 – Gwada yadda za a yi Nazain Littafi Mai Tsarki 40

**Shirin Allah Domin Almajirantad da Matasa - Kashi Biyu 43**

IV. Tabbatatun Almajirai Cikin Bishara ta Alheri Tsantsa 45

_______Nazari 8 – Tabbatatun Almajirai Cikin Bishara ta Alheri Tsantsa 45

V. Tabbatatun Almajirai Cikin Shirin Allah na har Abada 50

_______Nazari 9 – Tabbatatun Almajiri Cikin Shirin Allah na har Abada 50

VI. Tabbatatun Almajirai Cikin Gidan Allah 57

_______Nazari 10 – Tabbatatun Almajirai Cikin Gidan Allah 57

VII. Tabbatatun Almajirai Cikin da tare da Almasihu 66

_______Nazari 11 – Ran ka Cikin Almasihu 66

_______Nazari 12 – Ran ka Cikin Almasihu 70

_______Nazari 13 – Lokacin addu'a na Kowace rana tare da Ubangiji 77

_______Nazari 14 – Taimako Mai amfani domin Addu'a da Sujada 84

_______Kana 31 na Saduwa da Almasihu. 89

Karin Taimako cikin Tafiyar ka na kowace Rana tare da Ubangiji.

Tsarin Karatun Littafi Mai Tsarki Cikin Shekara 90


Takardan Shaidan Gamawa 93

# SHIRIN ALLAH DOMIN ALMAJIRANTAD DA MATASA = Kashi Daya




Amma Yesu ya ce, "Ku bar kanana
su zo wurina, kada ku hana su.
Ai mulkin sama na irin su ne"
Matiyu 19:14

Horaswa na Almajiranci zai taimaki Sabobin tuba ga Almasihu su zama da karfi cikin bangaskiyarsu. Wannan shine Littafin Nazari domin almajiranci. Wani lokaci mukan "hada da" ko lura da itace mara motsi ko itace mara karfi domin ya goyi baya lokacinda yana girma. Manufar mu cikin wannan nazari shine domin tafiya tare da sabon almajiri, da "hada da" domin fahimtar bangaskiyarka. Mun yi haka domin ka iya tsaya da karfi da kanka da zama da girma cikin bangaskiya (kamar kwatanci na itace da an nuna a zane a kasa).



**Sabo ko Itace Mara karfi**
**Horaswa na Almajiranci domin**
**Sabonbin Tuba**



**Tabbatacen Itace Mai Karfi Mai Ya'ya**
**Mai Bada Gaskiya day a yi Girma Zai iya**
**Tsay da Karfi**

# 1. IKON ALMAJIRI DA ISAN SU

## Nazari 1

## Maganar Allah Gaskiya ne, kuma Zan iya Gaskata ta.

### [Iko da Isan Maganar Allah]




**Sai mu bi da gina rayukanmu akan Maganar Allah (Littafi Mai Tsarki).** Idan ka gina rayuwarka akan wani abu dabam da Maganar Allah, zai fadi. Maganar Allah gaskiya ce, Amintacce, da cikake. Ya ba mu Maganarsa na Rai domin ya tanada kowane abin da mu ke bukata na rayuwa da Allah yana so mu rayu a ciki.

## <u>Ayohin Haddacewa:</u>

**2 Timoti 3:16-17**

***"Kowane Nassi hurarre na Allah ne, mai amfani ne kuma wajen joyarwa, da tsawatarwa, da gyaran hali, da kuma tarbiyyar aikin adalci, domin bawan Allah ya zama cikakke, shiryayye sosai ga kowane kyakkyawan aiki."***

**Karanta Farawa 1:1-3**

*"A cikin farko Allah ya halici sama da kasa. Kasa kuwa sarari ce, wofi kuma; a kan fuskar zurfi kuma sai duhu; ruhun Allah kuwa yana Tafiya a bisa ruwaye. Sai Allah ya ce, '**Bari haske shi kasance:' haske kuwa ya kasance.** Allah kuwa ya ga haske yana da kyau: sai Allah ya raba tsakanin haske da duhu. Allah ya ce da haske rana, duhu kuwa ya ce das hi Dare. Aka yi maraice aka yi safiya kuma, kwana na fari ke nan."*

Sai Allah ya kuma ce, ***'Bari sarari shi kasance a tsakanin ruwaye, shi raba ruwaye da ruwaye. Allah kuwa ya yi sarari, ya raba ruwayen da ke karkashin sararin da ruwayen da ke bisa sararin: haka kuwa ya zama.'*** Sa'annan Allah ya kira sararin Sama: aka yi maraice aka kuma safiya, kwana na biyu ke nan.

Sai Allah ya ce, ***'Bari ruwaye na karkashin sama su tattaru wuri daya, sandararriyar kasa kuwa ta bayyana:' haka kuwa ya zama.'*** Allah ya kira sandararriyar kasa Duniya: tattaruwan ruwaye kuma ya kira su Tekuna: Allah kuwa ya ga yana da kyau. Allah kuwa ya ce, ***'Bari kasa ta tsiro da ciyawa, da ganyaye masu-bada kwaya, da itatuwa masu-bada 'ya'ya kowane bisa ga irinsa, wanda kwayarsa tana ciki, a duniya:' haka kuwa ya zama.'*** Kasa fat a tsirar da ciyawa, da ganyaye masu-bada kwaya bisa ga irinsu, da itatuwa masu-bada 'ya'ya wadanda kwaya ke ciki, bisa ga irinsu: Allah kuwa ya ga yana da kyau. Akayi maraice aka yi safiya kuma, kwana na uku ke nan.

Kuma Allah ya ce, ***'Bari haskoki su kasance cikin sararin sama domin su raba tsakanin yini da dare; su zama kuma domin alamu, da wakatai, da kwanaki da shekaru: su zama kuma domin haske cikin sararin sama, su bada haske bisa duniya: haka kuwa ya zama.'*** Sa'annan Allah ya yi manyan haskokin nan biyu; babban domin shi yi mulkin yini, karamin domin shi yi mulkin dare: ya yi taurari kuma. Allah kuma ya sanya su cikin sararin sama domin su bada haske a bisa duniya, su yi mulkin yini da dare, su raba tsakanin haske da duhu kuma: Alah kuwa ya ga yana da kyau. Aka yi maraice aka yi safiya kuma, kwana na hudu ke nan.

Sai Allah ya ce, ***'Bari ruwaye su yawaita haifan masu-motsi wadanda ke da rai, suntsaye kuma su tashi birbishin duniya cikin sararin sama.' Sai Allah ya halici katayen abubuwa na teku, da kowane mai-rai wanda ke motsi, wadanda ruwaye suka haife su a yaiwace, bisa ga irinsu, kowane tsuntsu kuma mai-tashi sama ga irinsa:'*** Allah kuwa ya ga yana da kyau. Bayan wannan Allah ya albarkace su, yana cewa, Ku yalwata da 'ya'ya, ku ribu, ku cika ruwaye cikin tekuna, tsuntsaye kuma su ribbabanya cikin duniya. Akayi Dare aka kuma safiya, kwana na biyar ke nan.

Allah kuwa ya ce, **'Bari kasa ta fid da mai-rai kowane bisa ga irinsa, bisashe, da masu-rarrafe, da dabbobin duniya bisa ga irinsu:' Haka kuwa ya zama.** Allah kuwa ya yi dabbobi na duniya bisa ga irinsu, bisashe kuma bisa ga irinsu, da kowane abin da ke rarrafe a kasa bisa ga irinsa: Allah kuwa ya ga yana da kwau. Kuma Allah ya ce, Bari mu yi mutum a cikin sifarmu, bisa ga kamaninmu: su yi mulki kuma bisa kifaye na teku, da tsuntsaye na sama, da bisashe,

da kuma bisa dukan duniya, da kowane abu mai-rarrafe wanda ke rarrafe a bisa kasa. Allah fa ya halice mutum cikin kamaninsa, cikin kamanin Allah ya halice shi; na miji da ta mace ya halice su. Allah ya albarkace su kuma: Allah ya ce masu, ku yalwata da 'ya'ya, ku ribbabanya, ku mammaye duniya, ku mallake ta; ku yi mulkin kifaye na teku, da tsuntsaye na sarari, da kowane abu mai-rai wanda ke rarrafe a kasa. Allah kuma ya ce, Ga shi, na bada kowane ganye mai bada kwaya da ke bisa fuskar duniya duka, da kowane itace, wanda diyan itace mai-bada kwaya yana cikinsa; shi zama abincinku: Kuma na bada kowane ganye ga kowane dabba na duniya, da kowane tsuntsu na sama, da kowane abin da ke rarrafe a kasa wanda rai ke cikinsa shi zama abincinsu: Haka kuwa ya zama. Allah kuma ya duba kowane abin da ya yi, gas hi kuwa, yana da kyau kwarai. Aka yi maraice aka kuma safiya kuma, kwana na shidda ke nan."

## Amsa wadannan Tambayoyi:

- Littafi Mai Tsarki ya ce wanene ya halitci kome da kome? ________________________
- Ta yaya ya yi halittar? ______________________________________________________
- Kwana nawa ya dauka domin halittar kome da kome? ____________________________
- Wane dabba ka fi so? ________________________________________________________
- Za ka iya halitar dabba da ka ke so daga ba kome? _____________________________
- Ka iya yin dukan ababa da Allah ya yi cikin kwana Shida? ________________________
- Ko Allah ya yi kamar yana da wani babban iko? _________________________________
- Ko muna bukata mu saurari maganar Allah kamar wannan? ______________________

## Karanta Yahaya 1:1-4, 14

*"Tun fil'azal akwai kalma, kalman nan kuwa tare da Allah yake, kalman nan kuwa Allah ne. She ne tun fil'azal yake tare da Allah. Dukan abubawa sun kasance ta gare shi ne, ba kuma abin da ya kasance na abubuwan da suka kasance, sai ta game das hi. Shie ne tushen rai, wannan rai kuwa shi ne hasken mutane."*

*"Kalman nan kuwa ya zama mutum, ya zauna a cikinmu, yana mai matukar alheri da gaskiya. Mun kuma dubi daukakarsa, daukaka c eta makadaicin Da daga wurin Ubansa."*

## Amsa wadannan Tambayoyi

- Lokacinda Yahaya ya yi magana akan kalman, yana Magana akan wanene? __________
- Wanene Yesu? ___________________________________________________________
- Yesu yana nan da shigan aiki lokacinda an halitci duniay? ________________________
- Kalman nan kuwa ya zama____________. Me ake nufi da wannan? _________________

  ____________________________________________________________________

- Wanene Kalmar Rai da aka rubuta akai cikin I Yohanna 1:1 wanda ya ba mu rai na har abada idan mun gaskata da shi? ______________________

**1 Yahaya 1:1**
*"Shi da yake tun fil'azal yake nan, wanda muka ji muka gani da idonmu, muka duba, hannuwanmu kuma suka taba, a game da Kalmar rai."*

**Karanta 2 Timoti 3:16 – 17:**

*"Kowane Nassi hurarre na Allah ne, mai amfani ne kuma wajen koyarwa, da tsawartarwa, da gyaran hali, da kuma tarbiyyar aikin adalci, domin bawan Allah ya zama cikakke, shiryayye sosai ga kowane kyakkyawan aiki."*

**Amsa Wadannan Tamboyoyi:**

- Mene ne Littafi Mai Tsarki? ______________________
- An rubuta Littafi Mai Tsarki da kalmomin wanene? ______________________
- 2 Timoti 3:16 – 17 ya fadi abubuwa hudu da Littafi Mai Tsarki ya yi mana. Mene ne wadannan abubuwa hudu da Littafi Mai Tsarki ya yi mana?






1. ______________________
2. ______________________
3. ______________________
4. ______________________

**Abin Yi: Ranakun Halita--Gani/Abin Yi/Launi**

<u>Umurni:</u>

- *Sa alama dai dai a kowane Ranar Halita da launin hotuna

## <u>Ranakun Halita</u>

| | | |
|---|---|---|
| **Rana ___**<br>**Allah ya yi haske**<br> | **Rana ___**<br>**Allah ya yi sarari**<br> | **Rana ___**<br>**Allah ya yi kasa da teku,tsiro da itatuwa**<br> |
| **Rana ___**<br>**Allah ya yi rana, wata da taurari**<br> | **Rana ___**<br>**Allah ya yi tsunsaye da kifaye**<br> | **Rana ___**<br>**Allah ya yi dabbobi da mutane**<br> |

**Abin Yi 2: Cika in da ba rubutu**

Umarnai:

- Karanta kowane aya. Cika kalmomi da babu a inda ba rubutu
- Ka yi launin hotunan

# Mene ne kuma Kalmar Allah zai yi?




A Zabura 119:105, mene ne Kalman Allah ga sayawanka? ______________________



Irimiya 23:29, wane abu biyu Maganar Allah ke so? _____________ da _______________



A Irimiya 23:29, me Maganar Allah Kan yi? _______________________





A Ibraniyawa 4:12, Maganar Allah Kalmar __________ mai karfi, da "rarrabe tunanin a cikin _________________________ mu."

# Nazari 2

## Ruhu Mai Tsarki yana Taimakon mu da Ba mu Iko

## [Iko da Isan Ruhu]




Fentikos ya zama alamar zuwan Ruhu Mai Tsarki. Allah Uba ya aiko da Dansa, Yesu kamar Kalma da ya Bayyana kan ta cikin siffar mutum. Lokacinda Yesu ya koma Sama, ya yi alkawarin aika wa masu bada gaskiya gareshi Mai taimako wato Ruhu Mai Tsarki. Allah ya sa a zuciyar manzani da annabawa su rubuta Maganarsa Mai Tsarki, Littafi Mai Tsarki. Ruhu Mai Tsarki ya ba masu bada gaskiya iko na fahimta da biyaya da maganar Allah da rayuwa a yadda yana so su yi rayuwa.

## Ayan Haddacewa:

**Galatiyawa 5:16**
*"Maganata ita ce, ku yi zaman Ruhu ba kuwa za ku biye wa halin mutuntaka ba."*

### Karanta Ayyukan Manzani 1:6–11:

*"Su fa, da suka taru, suka tambaye shi, suka ce, Ubangiji, a wannan lokaci ne ka ke mayar wa Isra'ila da mulki? Ya ce masu, Ba naku ba ne da za ku san zamanu da wokatai wandanda Uba ya sanya a cikin nasa hukunci. Amma za ku karbi iko lokacin da Ruhu Mai Tsarki ya zo bisanku, za ku zama Shaiduna kuma cikin Urushalima da cikin dukan Yahudiya da Samariya, har kuma iyakan duniya.*

*Sa'ad da ya fadi wannan, su suna cikin dubawa, aka dauke shi bisa girgije ya karbe shi har ya bace wa ganinsu. Tun suna cikin zuba ido zuwa sama, ya tafiya, sai ga mutum biyu daura da su a tsaye da fararen tufafi; suka ce kuma, ku mazajen Galili, don me kuke tsaye kuna duba zuwa sama? Wannan Yesu wanda aka dauke shi daga wurinku, aka karbe shi sama, kamar yadda kuka ga tafiyarsa zuwa cikin sama, haka nan zai dawo."*

**Amsa wadannan Tambayoyin:**

- Ina ne Yesu zai tafi bisa wannan labari? ______________________________
- Yesu ya yi alkawarin aika wanene a gurbinsa bayan ya tafi? ______________________________

  ______________________________
- Mene ne Ruhu Mai Tsarki zai ba masu binsa? ______________________________

**Karanta Ayyukan Manzani 2:1 – 4**

*"Sa'anda ranar Fentikos ta yi, dukansu suna tare wuri daya. Ba labara, sai wani motsi kamar na hucin iska mai karfi ya fito sama, duk ya gama gida wurin da suke zaune. Harsuna kuma mararraba da juna, kamar na wuta, suka bayanu gare shi, ya zauna bisa kowane daya a cikinsu. Aka cika dukansu da Ruhu Mai Tsarki, suke soma zance da wadansu harsuna, yadda Ruhu ya ba su yin furci."*

**Amsa, wadannan Tambayoyi**

Yi tunani akan wannan muhimmiyar ranar Fentikos lokacinda almajiran Yesu sun karbi Ruhu Mai Tsarki. Ka yi kamar kana daya daga almajiran, Fadi da kuma rubuta akan ranar:



- Me ka ji?

______________________________



- Me ka gani?

______________________________



- Me ka karba?

______________________________

## Karanta Galatiyawa 5:16–17, 22–25:

*"Maganata ita ce, ku yi zaman Ruhu, ba kuwa za ku biye wa halin mutuntaka ba. Don halin mutuntaka gaba yake yi da Ruhu, Ruhu kuma yana gaba da halin mutuntaka. Wadannan biyu gaba suke yi da juna, har ba kuwa iya yin abin da kuke so".*

Albarkar Ruhu kuwa ita ce kauna, da farinciki, da salama, da hakuri, da kirki, da nagarta, da aminci, da tawali'u da kuma kamunkai. Masu yin irin wadannan abubuwa, ba dama shari'a ta kama su. Wadanda kuwa suke sun a Almasihu Yesu ne, sun giciye halin mutuntaka da mugayen sha'awace-sha'awace im im. In dai rayuwar tamu ta Ruhu ce, to, sai mu tafiyar da al'amuranmu ta wurin ikon Ruhu

## Amsa Wadannan Tambayoyi

- Mene ne Ruhu Mai Tsarki yana taimakon ba kada ka yi? ____________________________
- Ina kyawawan abubuwa tara da Ruhu Mai Tsarki ke ba masu bada gaskiya? ___________

  ________________________________________________________________________________

  ________________________________________________________________________________
- Galatiyawa 5:25 *"Mun samu sabon rai tawurin Ruhu. Saboda haka mu bi Ruhu."*

  Daga ina za mu samu sabon rai? ____________. Ya kamata mu bi wanene? ____________

**Abin yi 1:**

Za ka iya launin wannan shafin

Taimoko Domin Ganin Hawan Yesu Sama



Taimako Domin Ganin Fenticos



**Abin Yi 2:** Madaurin Fentikos

# <u>MADAURIN FENTIKOS</u>



<u>Umarnai: [Mai bi da kai zai iya taimakon ka]</u>

- Ka yi madaurin kai tawurin amfani da hoton harshen wuta na bisa.
- Yi launi da zai nuna harshen wutan.
- Domin a yi madaurin, ka yanka <u>strips</u> na takarda (wajen kusan 1" fadi 12" tsawo kowanne). Hada harshen <u>strips</u> tare domin ya zama madauri kewaye daya. Gwada da kan yaro kafin a hada. Hada harshen wutan a gaba da headband din.

**Abin yi 3: Cika inda ba rubutu**

Umarnai:

- Karanta kowane aya. Cika kalmoni da babu a inda ba rubutu ko ka amsa tambayoyi.
- Za ka yi launin hotuna.

# Mene ne kuma Ruhu Mai Tsarki Zai Yi?




A Yahaya 1:32-33, ga mene ne Yahaya ya kwantanta Ruhu Mai Tsarki? ______ ________________________________

Mene ne ma'anar wannan? __________



A Yahaya 7:37 – 39, *"Idan mutum ________ ciki na, kogunan ruwa rai _____________ za su gudana daga Daga zuciyarsa."*

Yesu yana Magana akan _________________



Ayyukan Manzani 1:8 ya bayyana Hoto da iko da Ruhu Mai Tsarki Ke ba masu bada gaskiya

____________________________

____________________________



A Galatiyawa 5:22-23 mene ne Ruhu Mai Tsarki ke yi domin taimakon masu bada gaskiya cikin rayuwansu? __________,

________, ________, _________, _________,


________, ________, _________, _________,

# II. BIYAYAN ALMAJIRI, ZAMAN MEMBA DA TUNI

## Nazari 3

## Allah yana so mu yi Baftisma kamar Yesus

### [Baftismar Ruwa]




**Lokacinda mai bada gaskiya ya yi baftisman ruwa, alama ce a sarari cewa mai bada gaskiya ya yi taraya cikin mutuwa, bizne da tashin Almasihu Yesu.** Yesu ya yi baftisma, Allah yana so masu bada gaskiya ma su yi baftisma domin tunawa da abin da Almasihu ya yi da abin da Ruhu Mai Tsarki ya yi masu.

## Ayan Hadacewa:

**Romawa 6:4**

*"Saboda haka, an binne mu da shi ken an, tawurin baftisma cikin mutuwarsa, domin kamar yadda aka ta da Almasihu daga matattu ta wurin daukakar Uba, haka mu ma mu yi zaman sabuwar rayuwa."*

**Karanta Matiyu 3:13-17:**

*"A lokacin nan ne Yesu ya zo daga kasar Galili, ya je kogin Urdun wurin Yahaya, domin ya yi masa baftisma.*
*Yahaya kuwa ya so ya hana shi, ya ce, "Ni da nake bukatar kai ka yi mini baftisma, ka zo gare ni?" Amman Yesu ya amsa masa ya ce, "Bari ya zama haka a yanzu, domin haka ne ya dace, mu cika dukan adalci." Sa'an nan Yahaya ya yarda masa. Da aka yi wa Yesu Baftisma, nan da nan da ya fito daga ruwan, sai ga Sama ta dāre, ya ga Ruhun Allah na saukowa kamar kurciya, har ya sauka kansa, sai aka ji wata murya daga sama ya ce, "Wannan shi ne Dana kaunatacce, wanda nake farin ciki da shi kwarai."*

**Amsa wadannan Tamboyoyi**

- Me Yesu yana so Yahaya ya yi masa? ____________________
- Me ya sa Yesu ya ce yana so a yi masa baftisma? ____________________
- Ta yaya Yahaya ya yi wa Yesu baftisma? ____________________
- Me Allah ya ce bayan an yi wa Yesu baftisma? ____________________

**Karanta Romawa 6:3-11:**

*"Ko kuwa kun rasa sani dukanmu da aka yi mana baftisma zuwa cikin Yesu Kristi, zuwa cikin mutuwatasa aka yi mana baftisma? Aka bizne mu fa tare da shit a wurin baftisma zuwa cikin mutuwa: domin kamar yadda aka tada Kristi daga matattu ta wurin darajar Uba.*

*Haka nan mu kuma mu yi tafiya cikin sabontakar rai. Gama idan mun hadu da shi bisa ga sifar mutuwatasa, za mu kuma kasance haka bisa ga sifar tashinsa; ana sane da wannan, aka giciye tsofon mutumin namu tare da shi, domin a kawar da jikin zunubi, domin da haka nan kada mu kara zama muna bauta wa zunubi; gama wanda ya mutu ya kubuta daga zunubi.*

*Amma idan muka mutu tare da Kristi, mun bada gaskiya za mu kuma rayu tare da shi; ana sane Kristi da yake ya tashi daga matattu ba shi koma mutuwa ba; nan gaba mutuwa ba ta da sauran mulki a kansa. Gama mutuwa da ya mutu, ya mutu ga zunubi sau daya: amman rai ka yake rayuwa, yana rayuwa ga Allah. Haka nan ku kuma ku maida kanku matattu ne ga zunubi, amman rayayyu ga Allah cikin Kristi Yesu."*

**Amsa Wadannan Tamboyoyi**

- Ko baftisma ruwa zai cece mu daga zunubanmu? ____________________

  ____________________

  ____________________

- Baftisma na ruwa ya nuna kasancewar mu ____________________ cikin Almasihu.
- Me ya sa masu bada gaskiya za su yi baftisma kamar Yesu? ____________________

  ____________________

  ____________________

**Abin yi 1:Hoto/Launi**



Ka iya yin launin wannan shafi




## Baftisman Yesu



**Abin yi 2:Cika inda ba Rubutu**

# <u>Mutuwa, Bizne da Tashi daga Mutuwa</u>

**A wannan nazari mun koya cewa:**

- Tubanmu daga zunubi yana nuna alaman (tsaya akan) mutuwar Yesu akan giciye.
- Shiga cikin ruwa alamar bison Yesu.
- Fitowarmu daga ruwa alamar tashin Yesu (dawo da rai kuma).

<u>Umarnai:</u>


- Sa lamba akan Magana da ya yi dai dai da kowane hoto a layi da an ja a kalkashin hoton.
    1. Tuban mu daga zunubi
    2. Mutuwar Yesu akan giciye
    3. Shiganmu cikin ruwa
    4. Jana'izan Yesu
    5. Fitowarmu daga ruwa
    6. Tashin Yesu (dawowa da rai kuma)

# Nazari 4

# Masu bada gaskiya su na cikin Jikin Almasihu

## [Membobin Juna]





Idan mun amince da gafar zunubanmu cikin Almasihu da karban Ruhu Mai Tsarki domin ya taimake mu, za mu kuma samu wata kyauta mai ban mamaki. **Mun zama gaban Jikin Almasihu wanda ma ana kira 'iyalin Allah, mutanen Gida Allah, ko Ikkilisiya.** Wannan kungiya ya hada dukan wadanda ke masu bin Almasihu ko ina a duniya. Mu ba kadai ba ne, yanzu mu gaba na iyalin Allah kungiyan masu bada gaskiya.

## Ayan Hadacewa:

**I Korintiyawa 12:12**

*"Wato, kamar yadda jiki yake guda, yake kuma da gabobi da yawa su gabobin kuwa ko da yake suna da yawa, jiki guda ne, to, haka ga Almasihu."*

## Karanta I Korintiyawa 12:12 – 27

*"Gama kamar yadda jiki daya ne, yana kuwa da gababuwa da yawa, dukan gababuwan jiki fa, ko da ya ke da yawa ne, jiki daya ne haka nan kuma Kristi ne. Gama cikin ruhu daya aka yi mana duka baftisma zuwa cikin jiki daya, ko Yohudawa ne ko Hellenawa ne, ko bayi ne ko yaya ne; duka kuwa a Ruhu daya aka shayar da mu.*

*Gama jiki ba gaba guda ba ne, da yawa ne. Idan kafa t ace, Da ya ke ni ba hannu ba ce, ba gaban jiki na ke ba; ba don wannan ta zama ba gaban jiki ba ce. Idan kunne ya ce, Da ya ke ni ba ido ba ne, ba gaban jiki na ke ba; ba domin wannan ya zama ba gaban jiki ba ne. Da a ce dukan jiki ido ne, ina ji? Da duka ji ne, ina sunsuna? Amma yanzu Allah ya sanya gababuwa kowane daya a cikinsu cikin jiki, yadda ya gamshe shi. Da a ce dukansu gaba guda ne, ina jiki? Amma yanzu gababuwa da yawa ne, jiki kuwa daya.*

*Ido kuwa ba shi da iko shi ce wa hannu. Ba ni bukatarka: ko kuwa kai ya ce wa kafafu, Ba ni bukatarku. Ba kuwa haka kadai ba; har ma wadannan gababuwa da ake ganinsu kamar raunana bukatattu ne: Wadannan gababuwan jiki fa da mu ke maishe su kamar marasa-daraja, mu kan bada mafificiyar daraja garesu; har gababuwanmu da suke munana suna samun mafificin kyaun gani; da shi ke gababuwanmu masu-kyau ba su da bukata ba: amma Allah ya harhada jiki, yana kara mafificiyar daraja ga gaban da ya ke tauyeye; domin kada tsaguwa ta kasance a jiki, amma dukan gababuwa su yi wa juna tattali daya Idan gaba daya kuwa ya sha radadi, dukan gababuwa suna shan radadi tare da shi; ko kuwa gaba daya ya sami girma, dukan gababuwa suna murna tare da shi.*

*Ku fa jikin Kristi ne, kowane kuwa gaba ne daga ciki."*

**Amsa Wadannan Tambayoyi:**


- Dole masu bada gaskiya su lura da juna da tuna da wadansu kafin ___________________
- Idan ka buga yatsanka da guduma, me dayan hanunka zai yi domin ya sa yatsan ya samu lafiya? (Nan da nan zai shafa abu a hanun da ya samu rauni. Bar yara su amsa da kansu.) ___________________________________________________________________
- Hanya daya ne, idan wani a jikin yana shan wahala, dukan membobi za su ___________ ________________________________________________ idan memba daya ya samu girma, dukan sauran memobi za su ______________________________________ domin mutumin.

**Abin yi 1:  Hoto/Launi**

Ka iya yin launin wannan

# Jikin Yesu Almasihu

## Jiki Daya/Gabobi Dayawa



**I Korintiyawa 12:12**


***"Wato, kamar yadda jiki yake guda, yake kuma da gabobi da yawa su gabobin kuwa ko da yake suna da yawa, jiki guda ne, to haka ga Almasihu."***

**Abin yi 2: Shafin Aiki Game da Jikin Almasihu**

Umarnai:

- Karanta ayoyi da ke kalkashi kowane hoto.
- Amsa tambayoyi kowane Magana daga littafin

# Shafin Aiki Game da Jikin Almasihu





**Karanta Afisawa 2:12 – 19** **Karanta I Korintiyawa 12:12-14; 27**

1. Rubuta cikin kalmominka abin da ka koya akan batattu da ke waje da jikin Almasihu daga Afisawa 2:12-19.

_______________________________________________

_______________________________________________

_______________________________________________

_______________________________________________

_______________________________________________

2. Rubuta cikin kalmominka abin da ka koya akan jikin Almasihu daga I Korintiyawa 12: 12-14, 27.

_______________________________________________

_______________________________________________


_______________________________________________

_______________________________________________

_______________________________________________

# Nazari 5
# Yesu yana so mu ci Jibin Ubangiji

## [Jibin Ubangiji]




**Yesu ya kasance tare da almajiransa a daren sa na karshe, ya ba su abinci ta musamman. An kira shi Jibin Ubangiji:** ya ba almajiransa gurasa da kokon domin tunawa da jikinsa da jininsa da zai bada shi hadaya lokacin da ya mutu domin zunubanmu. Mu da muke masu bin Almasihu za mu ci Jibin Ubangiji domin tunawa da shelar abin da Yesu ya yi mana akan giciye har kafin ya dawo. Shine Ragon Hadaya namu. Ya zub da jininsa akan giciye, ya mutu ya kuma tashi domin ya ba mu Sabon Alkawari, ko Sabon Alkawari daga Allah, domin mu zama sabon halitta cikinsa.

**<u>Ayan Hadacewa:</u>**
**Luka 22:19-** ***"Sai ya dauki gurasa, bayan da ya yi godiya ga Allah, ya gutsuttsura ya ba su, ya ce, 'Wannan Jikina ne da za'a bayar dominku. Ku rika yin haka domin tunawa da ni.'"***

**<u>Karanta Fitowa 12:21-30</u>**

*"Sa'annan Musa ya kirayi dukan dattibai na Isra'ila, ya ce masu. Je ku, ku dauki yan raguna gwargwadon iyalanku, ku yanka Faska. Ku dauki kilili na zofa, kuma ku tsoma cikin jinin da ke cikin tasa, ku shafa dokin kofa na bisa da dogaran kofa da jinin da ke cikin tasa; kada kowane a cikinku shi fita kofar gidansa sai safiya ta yi. Gama Ubangiji za ya ratsa ta tsakiya domin ya buga Masarawa; amma sa'anda ya ga jinin a bisa dokin kofa da bisa dogaran kofa biyu, Ubangiji za ya ketare wannan kofa, ba kuwa za ya bar mai-halakaswa ya shiga cikin gidajenku garin ya buge ku ba.*

*Za ku kiyayi wannan al'amari farilla a gare ka da 'ya'yanka har abada. Za ya zama kuwa, sa'anda kun rigaya kun zo cikin kasa wanda Ubangiji za ya ba ku, bisa ga alkawarin da ya yi, za ku kiyayi wannan hidima kuma. Zai faru kuma, sa'anda 'ya'yanku za su ce maku. Menene dalilinku da wannan ibada? Za ku ce, Hadaya ce ta faskar Ubangiji, da ya ketare gidajen*

*'ya'yan Isra'ila cikin Masar, sa'anda ya bugi Masarawa, ya ceci gidajenmu kuma. Mutanen fa suka sunkuyar da kai, suka yi sujada. 'Ya'yan Isra'ila suka tafi suka yi wannan; kamar yadda Ubangiji ya umurta ga Musa da Haruna, haka suka yi.*

*Ananan da tsakiyar dare, sai Ubangiji ya bugi dukan 'ya'yan fari cikin kasar Masar, daga dan fari na Fir'auna da ke zaune bisa kursiyinsa, zuwa dan fari na daurarren da ke cikin kurkuku; da dukan 'ya'yan fari na dabbobi. Fir'auna kuwa ya tashi da dare, da shi, da dukan bayinsa, da dukan Masarawa; aka yi kuka mai-zafi cikin Masar; gama babu gida inda ba matace."*

**Amsa Wadannan Tambayoyi:**

- Me ya sa Musa ya ce wa 'ya'yan Isra'ila su shafa jinin dan rago akan dogaran kofofin gidajensu? Ya zama kamar abin mamaki a yi abu haka. ______________________________

  ______________________________________________________________________
- Me ya faru da Masarawa da ba su shafi jinni a dogaran kofofinsu ba? _______________

  ______________________________________________________________________
- Me ya faru da iyalan Isra'ilawa da sun shafa jinin a dogaran kofofinsu? _____________

  ______________________________________________________________________

**Karanta Matiyu 26:26-28**

*"Suna cikin cin abinci, sai Yesu ya dauki gurasa, ya yi godiya ga Allah, ya gutsuttsura, ya ba almajiran, ya ce, "Ungo, ku ci. Wannan jikina ne."*
*Sai ya dauki koko, bayan ya kuma yi godiya ga Allah, sai ya ba su, ya ce, "Dukkanku ku shassha. Wannan jikina ne na tabbatar alkawari wanda za a zubar saboda mutane da yawa, domin gafarar zunubansu."*

**Amsa Wadannan Tambayoyi**


- Me Yesu ya ce gurasa ya wakilta? ______________________________________
- Me Yesu ya ce kokon ya wakilta? ______________________________________
- *Karanta Luka 22:19. Me ya sa Yesu ya ce masu bada gaskiya su ci Jibin Ubangiji?*
  *"Sai ya dauki gurasa bayan da ya yi godiya ga Allah, ya gutsuttsura, ya ba su, ya ce, "Wannan Jikina ne da za a bayar dominku. Ku rika yin haka, domin tunawa da ni."*

  ______________________________________________________________________
- Cin Jibin Ubangiji yana taimakonmu tuna da Yesu Ragon Hadaya namu wanda ya mutu a madadin mu. Jibin Ubangiji ba ya ceto, kamar yadda baftisma ba zai cece mu ba. Meme ne zai cece mu? ______________________________________________
- Allah yana so mu ci gaba da cin Jibin Ubangiji kamar masu bada gaskiya domin kada mu? ________________________________________________________

**Abin yi 1: Hoto/Launi**

Za yi Launin wannan shafin

# Yesu, Dan Ragon Ketarewanmu



*"Ku ga, ga Dan Rago na Allah, wanda zai dauke zunubin duniya"*

Yahaya 1:29[b]

**Abin yi 2: Cika inda ba Rubutu: Jibin Ubangiji**

Umarnai:

- Karanta ayoyi na hotunan. Cika inda ba rubutu daga littafin


# Jibin Ubangiji



**Fitowa 12:23** [Ubangiji] zai ga jinin a bisa kan kofar, da dogaran kofa duka biyu" sai Ubangiji zai _______ ______________________________



**I Korintiyawa 5:7b**: "Domin Almasihu, namu_____ ______________________________________ an kashe domin tsabtace mu."



**I Korintiyawa 11:23-24**: "Ubangiji Yesu, a daren da aka bashe Shi, ya dauki gurasa, bayan da ya yi godiya ga Allah kuma, sai ya gutsutsura, ya ce, 'Wannan ____________ na ne"




**I Korintiyawa 11:25b**: "Ya dauki Kokon nan na Sabon Alkawari ne, ya fara da __________________ mutuwa ta"



**I Korintiyawa 11:12-25**: "Yesu ya ba almajiransa Gurasa da Kokon su ci da sha, ya ce masu ku rika yi haka ______ _________________________________"

# III. ALMAJIRAN DA SUN KAFU CIKIN NAZARIN LITTAFI MAI TSARKI

## Nazari 6
## Yadda za ka yi Nazarin Littafi Mai Tsarki




**Mun koya cewa Allah ya ba mu Littafi Mai Tsarki domin ya taimake mu rayuwa domin sa.** Domin mu yi haka, dole sai mun san yadda za mu yi nazarin Littafin domin mu koyi abin da Allah yana so mu yi. Akwai muhimman matakai hudu da za mu iya amfani da su domin nazarin cikin Littafi Mai Tsarki. Matakan su ne: Kula, Tunani, Tattaunawa da Aikatawa.

### Ayan Hadacewa:

*Yahaya 14:26. "Amma Mai Taimako, Ruhu Mai Tsarki, wanda Uba zai aiko da sunana, shi ne zai koya muku kome, ya kuma tuna muku duk abinda na fada muku."*

**Karanta Ayyukan Manzani 8:26-38**

*"Amma mala'ikan Ubangiji ya yi magana da Filibus, ya ce, Tashi, ka nuna wajen kudu zuwa karabka wada ta fita daga Urushalima zuwa Gaza: jeji ke nan. Ya tashi ya tafi: sai ga wani mutummin, Itiyofiya (Habasha), bābā ne, mai-sarauta da yawa karkashin Kandis, sarauniyar Habashawa, wanda kayan ajiyarta duka suna hannunsa, ya zo Urushalima ke nan garin yin sujada; yana kan komawa, yana zaune cikin karusarsa, yana karatun annabi Ishaya. Sai Ruhu ya ce wa Filibus, Ka gusa, ka hadu da wannan karusa.*

*Filibus ya yi gudu zuwa wurinsa, ya ji shi yana karatun annabi Ishaya, ya ce, Ka fahimci abin da ka ke karantawa? Yace, Yaya zan iya, sai ko wani ya bishe ni? Ya roki Filibus ya hau, ya zauna tare da shi. Nassin littafi inda ya ke karantawa ke nan,*

> *'Aka ja shi kamar tunkiya zuwa wurin yaka; Kamar yadda dan rāgo kuma a gaba mai-saisaya yana shiru, Haka nan bai bude bakinsa ba: Cikin kaskantassa aka kwace masa shari'a.'*

*Wa za ya bada labarin tsararsa? Gama an dauki ransa daga duniya. Babān ya amsa wa Filibus, ya ce, Ina bida gare ka, Annabi yana ambaton wanene? Kansa ne, ko wani ne? Filibus ya bude bakinsa, ya soma tun daga wannan nassi, ya yi masa wa'azin Yesu. Ananan suna cikin tafiyarsu, suka zo wurin wani ruwa; bābān ya ce, Ga ruwa; me zai hana a yi mini baftisma? Filibus ya ce, Idan ka bada gaskiya da dukan zuciyarka, sai ka yi. Ya amsa ya ce, Ina bada gaskiya Yesus Kristi Dan Allah ne. Ya umurta a tsaida karusa: su biyu fa suka sauko, suka shiga ruwa, da Filibus da bābān; ya yi masa baftisma."*

**<u>Amsa Wadannan Tambayoyi:</u>**

- Lokacin da Filibus ya samu mutumin Habasha, menene mutumin ke yi? ______________

  ______________________________________________________________________________
- Mutumin ya gane abin da yana karatu? ____________________________________________
- Mutumin ya tambayi wane ne domin ya taimake shi gane abin da yana karatu? _______

  ______________________________________________________________________________
- Me Filibus ya ce wa mutumin? __________________________________________________
- Me mutumin ya yi bayan ya ji Bishara Mai Dadi? _____________________________________

  ______________________________________________________________________________

**<u>Nazarin Littafi Mai Tsarki:</u>**

- Me ya fi al'ajibi da shaida Bishara Mai Dadi (Bisharan Yesu Almasihu) da taimakon wani ya zama mai bada gaskiya ga Almasihu.
- Wannan labari ya nuna mana muhimman umarnai hudu a yadda za mu yi nazarin Littafi Mai Tsarki da za ka yi amfani da su lokacinda kana nazarin Littafi Mai Tsarki za mu yi amfani da su a Nazari ta 7 na Littafi Aiki.

**<u>Matakai Hudu na Zanarin Littafi Mai Tsarki Su ne</u>:**

1. **"Duba shi" (Lura) – Me ya ce?**
   (aya 28 …" *yana komawa (mutumin Habashan) gida a zaune a cikin keken dokinsa yana karatun Littafin Annabi Ishaya)".*
   **Karanta ayan sau da yawa. Tambayi kanka: me ke faruwa? Ya shafi wanene? Ina da wani lokaci abin ya faru?**

2. **"Yi Tunani akai" (Tunani)- Mene ne ya ke nufi?**
   (aya 30 – *"Filibus ya yi gudu zuwa wurinsa, ya ji shi yana karatun Littafin Ishaya. Ya ce, "kana kuwa fahimtar abin da kake karantawa?"*
   **Tambayi kanka: Me Allah yana so in sani daga wannan wurin?**

3. **“Yi Magana akai” (Tattauna)- Me wadansu ke fadi?**
   (aya 31-38- Sai ya ce, *“ina fa? Sai ko wani ya fassara mini.” Sai ya roki Filibus ya hau su zauna tare, wannan kuwa shi ne nassin da yake karantawa, “An ja shi kamar tunkiya zuwa mayanka kamar yadda dan rago yake shiru a hannun mai sausayarsa, hana, ko bainsa bai bude ba. An yi masa kaskanci har an hana masa gaskiya ta sa. Wa yake iya ba da labara zamaninsa? Domin an katse ransa daga duniya. Sai bābān ya ce wa Filibus, “Shin kam Annabin nan, maganar wa yake yi? Tasa ko ta wani?” Sai Filibus ya bude baki ya fara da wannan Nassi yana yi masa bisharar Yesu.”*
   **Yi Magana akan wannan wurin tare da wadansu amintattun masu bada gaskiya.**

4. **“Aikatawa” (Aikatawa)- Ta yaya zan aikata shi a rayuwa ta?**
   (aya 3$^{b}$ – 38 – *“Suna cikin tafiya, suka iso wani ruwa sai bābān ya ce, ka ga ruwa! Me zai hana a yi mini baftisma?”*
   *Filibus ya ce, “in dai ka ba da gaskiya da zuciya daya, ai, sai a yi maka.” Bābān ya amsa ya ce, na gaskata Yesu Almasihu dan Allah ne.”*
   *Sai ya yi umurni a tsai da keken dokin. Sai kukan su biyu suka gangara cikin rowan, Filibus da bābān, ya yi masa baftisma.”*
   **Ka sake cikin rayuwanka bisa a abinda wannan wuri ya ce.**

- Tuna da Matakan nan Hudu Motion Activities.
  - Yin amfani da motsin hannu zai tamakae ka tuna kowane matakai hudu na nazarin Littafi Mai Tsarki?
    1 “Duba shi” (nuna zuwa idanu); 2 “Tuna shi” (nuna zuwa kai); 3. “Yi Magana akai” (nuna zuwa baki); 4. “Aikata shi” (Mika hannu).
  - Gwada sake amfani da mataka ta motsa hannun.

**Abin yi 1: Hoto/Launi**

Za ka iya launin shafin

## <u>Filibus da Mutumin Habasha</u>



**Ayyukan Manzani 8:30-31**


*"Sai Filibus ya yi gudu zuwa wurinsa, ya ji shi yana karatun*
*Littafin Annabi Ishaya. Ya ce, "kana kuwa fahimtar abin da kake karantawa?*
*Sai ya ce, "Ina fa? Sai ko wani ya fassara mini".*
*Sai ya roki Filibus ya hau su zauna tare.*

**Abin yi 2: Matakai Hudu na yadda za a yi Nazarin Littafi Mai Tsarki.**

Umarnai:

- Duba Matakai 4 na Nazarin Littafi Mai Tsarki.
- Rubuta Matakai 4 na Nazarin Littafi Mai Tsarki cikin in da ba rubutu a kujeran nan.
- Yi launin kowane sashe na kujeran bisa shiyyan a kasa.

## Matakai Hudu na yadda za a yi Nazarin Littafi Mai Tsarki Rubuta Kalmomin akan Kujeran



Kafa #1 shine **Duba (Duba shi)**- Rubuta Duba a kofan sai ka yi launin kafar da shudi

Kafa #2 shine **Tunani (Yi Tunani a kai)**- Rubuta Tunani a kafan sai ka yi launin kofar da Ja

Kafa #3 **Tattauna (Tattauna a kai)**- Rubuta Tattauna a kofar sai ka yi launin kofar Da kore

Mazaunin shi ne **Aikatawa (Aikata shi)**- Rubuta Aikatawa akan mazaunin sai ka yi launin mazaunin da Rawaya

**Abin yi 3: Nazarin Matakai na Littafi Mai tsarki**

Umurnai:

- Karanta kowane aya kasa da hotunan. Cika filin da ba rubutu bayan tambayoyin
- Ka yi launin hotunan.

# Nazarin Matakai na Littafi Mai Tsarki daga Ayyukan Manzani 8



**Ayyukan Manzani 8:28 –** Duba shi: Mutumin Habasha yana duba me?
______________________________



**Ayyukan Manzani 8:30-31**
Yi Tunani a kai: Me mutumin Habasha ke bukata?______________________



**Ayyukan Manzani 8:26-39**
Tattauna a kai, Idan mun iya, yi Magana da wani dabam akan wannan Labara. Rubuta wani shawara da suke Da shi____________________________
__________________________________
__________________________________



**Ayyukan Manzani 8:36-37[a]**
Aikata shi! Mutumin Habasha ya gaskata ya kuma so a yi masa baftisma nan da nan. Ta yaya za ka mori wadannan ayoyin da labara domin rayuwarka yanzu?__________
_________________________________

# Nazari 7

Gwada yadda za a yi Nazarin Littafi Mai Tsarki muna bukatar Littafi Mai Tsarki domin mu san yadda za mu yi wa Allah biyaya a rayuwarmu. Muna bukata mu san yadda za mu karanta da yin Nazarin Littafi Mai Tsarki domin Allah ya yi Magana da mu tawurin kalmansa.

**Ayan Hadacewa:**
**Markus 1:35**
*"Da asussuba ya tashi ya fita, ya tafi wani wuri inda ba kowa, ya yi addu'a a can".*

**Karanta Markus 1:35**
*"Da asussuba ya tashi ya fita, ya tafi wani wuri inda ba kowa, ya yi addu'a a can".*

**Amsa Wadannan Tambayoyi:**

- Yi amfani da matakai Hudu na Nazarin Littafi Mai Tsarki domin ka yi nazarin Markus 1:35.

**(Ayan Hadacewa)**
Cika filaye da ba rubutu a kasa da amsoshinka. Mai bi da ku zai iya taimakon ka.

## MATAKAI HUDU NA NAZARIN LITTAFI MAI TSARKI

**1.** **"<u>DUBA SHI</u>" (DUBA)- Mene ne ya ce?**

- Karanta abin da Littafi Mai Tsarki ya ce, yi addu'a Ruhu Mai Tsarki zai taimake ka ka ga abinda Allah yana cewa lokacin karatun.
- **Duba:** Karanta Markus 1:35- Ka duba abinda ke taruwa, wa ya shafa, ina ya ke faruwa da wani lokaci ya faru. Yanzu, rubuta amsoshinka bisa abinda ka gani a kasa:

________________________________________

________________________________________

**2.** **"<u>YI TUNANI A KAI</u>" (TUNANI)- Me wannan wuri cikin Littafi Mai Tsarki ke nufi?**

- Yi tunani akan abin da wannan sashen Littafi Mai Tsarki ke nufi. Yi addua'a Ruhu Mai Tsarki ya taimake ka gane ta. (Tuna, idan kana yin wannan da wadansu ne, mataki na 2 da mataki na 3 za su tafi tare.
- **Tunani:** Bisa ga abin da ka karanta (a dubawarka) daga Markus 1:35, a tunaninka su sani? Me ya sa an rubuta wannan cikin Maganar Allah? Yanzu, ka rubuta tunanink akan wadannan tambayoyin a kasa.

________________________________________

________________________________________

3. **“TATTAUNA A KAI” (TATTAUNAWA)-** Me wadansu sun ce?

- Nemi abin da wadansu sun yi tunani da abin da sun ce akan wannan wurin ka yi addu’a Ruhu Mai Tsarki zai taimake ka ka kaya daga wadansu. (Ka tuna, idan wannan nazari domin kanka ne, mai yiwu wa ba za ka yi amfani da mataki na 3 ba).

- **Tattaunawa:** Kwatanta abin da ka koya daga Markus 1:35 da abin da ka dandano a rayuwar ka da na wadansu a yau. Me ya zama daidai ko bambanci daga ganewwarka da nasu? Me ya zama daidai ko dabam daga aikatawa naka da na Yesu?
  Ka rubuta amsoshin tambayoyin kasa.

________________________________________________________

________________________________________________________

4. **“AIKATA SHI” (AIKATAWA)-** Ta yaya zan iya aikata a rayuwa ta?

- Yi shawaran abin da za ka yi ra’ayoyi na wannan wurin cikin rayuwanka da addu’a domin Ruhu Mai Tsarki ya taimake ka.
- **<u>Aikatawa:</u>** Maganar Allah zai iya nuna mana yadda za mu rayu kowace rana domin mu zama kamar Almasihu. Allah yana amfani da Ruhu Mai Tsarki domin ya taimake mu fahimtar Maganarsa da aikatawa a rayuwar mu.
  Ta yaya za ka yi amfani da abin da ka koyo daga Markus 1:35 domin ya taimake ka ka zama kamar Almasihu?
  Wane sakewa kana bukata a ranka?
  Yanzu, rubuta amsoshin tambayan a kasa.

________________________________________________________

________________________________________________________


**Abin yi 1: Zana kanka kana Nazarin Littafi Mai Tsarki ka launa shi.**


<u>Umurnai</u>: [Mai bi da kai zai iya taimake ka da wannan abin yi]

- Yesu yana so mu dauki lokaci muna nazarin Maganar Allah da koyaon yadda za mu yi rayuwa kamar masu bin Yesu Almasihu.
- Zana hoton kanka kana zanarin Littafi Mai Tsarki, ka kuma yi launin hoton.

## Zana kanka kana Nazarin Littafi Mai Tsarki

# Shirin Allah Domin Almajirai Matasa – Sashe Biyu





**Sabo ko Itace Mara karfi Horaswa na Almajiranci domin Sabonbin Tuba**

**Tabbatacen Itace Mai Karfi Mai Ya'ya Mai Bada Gaskiya day a yi Girma Zai iya Tsay da Karfi**

Manzo Bulus ya rubuta wasiku 13 ga Ikkilisiyoyi da ke tasowa. Wadannan wasiku suna cikin Litattafan Sabon Alkawari na Littafi Mai Tsarki. Ya rubuta wadannan wasiku domin taimakon masu bada gaskiya cikin wadannan Ikkilisiyoyi, membobin iyalin Gidan Allah su yi karfi cikin bangaskiyarsu, karfi cikin Maganar Allah, da cika da karfi domin tsayaya gaba da malaman karya.

Bulus ya rubuta wasiku ko'ina cikin aikinsa na Ikkilisiya. An sansu kamar fari, tsakiya, da wasiku na karshe. An rubuta wadannan cikin tsari da manufa dabam dabam.

- Wasiku na Fari an yi amfani da su domin a tabbatar da tsare Bishara ta Alheri Tsantsa. Galatiyawa, I da 2 Tassalonikawa, I da 2 Korintiyawa, Romawa.

- Wasiku na Tsakiya an yi amfani da su a Ikkilisiyoyi domin su zama da tunani daya cikin Manufa da Shirin Allah na har Abada. Afisawa, Filibiyawa, Kolosiyawa, Filiman.

- Wasiku na Karshe an yi amfani da su domin sa iyalin gidan Allah. I Timoti, Titus, 2 Timoti.


Littafi Mai Tsarki ya kira Bulus “Gwani Magini” (I Korintiyawa 3:10). Wasikunsa kamar kaya ne da magini zai yi aikin ginin gida da shi. Kayan ginin Bulus domin “ginawa” ko karfafa sabobin tuba ne cikin Iyalin Gidan Allah. Su na da amfani domin gina almajirai na Almasihu.

Kamar misali, Wasikar Bulus na Fari zuwa ga Galatiyawa ya zama zarto. Afisawa, Wasika na Tsakiya, zai zama guduma. Wasiku na karshe, I da 2 Timoti, zai zama murabba.










Kowanne cikin wadannan wasiku (Ko Litattafan Sabon Alkawari) na da manufa na **<u>gina ginshikin Iyalin Gidan Allah</u>** kamar sabon tuba, kai memba ne na Iyalin ko Gidan Allah.


Kamar yadda dole kafinta ya san yadda zai yi aiki domin gina gida mai karfi, haka ma almajiri matashi dole ya san yadda zai yi aiki da maganar Allah domin ya yi girma da karfi da tabbaci cikin bangaskiya da taimakon wadansu su yi girma.

**Galatiyawa** daya ne daga **Wasiku ta Farko** na Bulus. Kayan aiki ne domin taimakon koyawa almajirai Bisharan Alheri na Tsantsa cikin Yesu Almasihu (dubi Sura 8). **Afisawa** daya ne daga **Wasiku ta Tsakiya** na Bulus. Kayan aiki ne domin taimakon koyawa almajirai Manufa da Shirin Allah (dubi Sura 9). **I Timoti** daya ne daga **Wasiku ta Karshe**. Zai taimaka koyadda almajirai cikaken Tsari na Iyalin Gidan Allah (dubi Sura 10).

Sauran surori cikin wannan Littafin aiki ya tanada Karin labarai da hanyoyin da zai taimaki almajirai matasa su karfafa cikin Ubangiji da zama masu bada ya’ya cikin shaida ma wadansu maganar Ubangiji.

# IV. Tabbatatun Almajirai Cikin Bishara na Alheri Tsantsa
# Lesson 8
# God Saves Us by His Grace Alone
## [Tabbatatun Almajirai cikin Bishara na Alheri Tsantsa]

## Iyalin Allah




An ba mu ceto da yanci **cikin alherin Almasihu tawurin bangaskiya ga Allah kadai.** An cece mu tawurin dogara cikin Yesu Almasihu kadai domin ya gafarta zunubanmu ba tawurin yin ayyuka masu kyau ba ne, kiyaye doka ko wadansu abubuwa ba. Mun hadu a Iyalin Gidan Allah tawurin Alherin Allah Tsantsa kadai. Dole mu yi rayuwa tawurin alherin kowace rana ba ta ayyuka ko bin doka ba. **Dole mu roki Ruhu Mai Tsarki ya taimake mu rayuwa domin Yesu Almasihu tawurin alheri da an ba mu.**

**Ayan hadacewa:**
**Galatiyawa 4:4–5**
*“Amma da lokaci ya yi sosai sai Allah ya aiko Dansa, haifaffen mace, haifaffe kuma a karkashin Shari’a, domin ya fanso wadanda suke a karkashin shari’a, a mai da mu a matsayin ya’yan Allah.”*

**Karanta Galatiyawa 3:1-5 (Bisharan Alheri Tsantsa)**
*“Ya Galatiyawa marasa-wayo, wanene ya yi maku maita, ku da aka nuna Yesu Kristi a sarari giciyeye a gaban idanunku? Wannan kadai na ke so in tambaya a gare ku. Ta wurin ayyukan shari’a kuka harbi Ruhu, ko kuwa ta wurin labara na bangaskiya? Kuna da wauta haka? Bayan da kun fara cikin Ruhu, yanzu kuna karasawa cikin jiki? Kun jimre da abu dayawa haka kauwai? In dai lallai kauwai ne. Shif fa wanda yake ba ku Ruhu, yana kuwa aika ikoki a cikinku, ta wurin ayyukan shari’a ne, ko kuwa ta wurin labara na bangaskiya?”*

**Amsa Wadannan Tambayoyi:**

- Ta yaya kirista na Galatiya sun zama masu bada gaskiya? ____________________________
- Sun yi kokari rayuwa tawurin bin doka cikin karfin su bayan an cece su? _____________

  ______________________________________________________________________________
- "Ko ya kamata mu yi kokarin rayuwa kamar masu bada gaskiya muna amfani da karfin da kuma karfinmu? ________________________________________________________________

<u>**Karanta Galatiyawa 2:16 (Alheri da Doka)**</u>

*"Da yake mun sani mutum baya samun kubuta ga Allah ta wurin bin shari'a, sai da ita wurin gaskatawa ga Yesu Almasihu kadai, mu ma mun gaskata da Almasihu Yesu, domin mu sami kubuta ga Allah ta wurin bangaskiya ga Almasihu, ba ta wurin bin shari'a ba, don ba dan Adam din da zai sami kubuta ga Allah ta hanyar bin shari'a."*

<u>**Karanta Galatiyawa 3:11-12 (Alheri da Ayyuka)**</u>

*"To, a fili yake, ba mai samun kubuta ga Allah ta wurin bin shari'a, domin "wanda yake da adalci ta wurin bangaskiya zai rayu. Shari'a kuwa ba ta dangana ga bangaskiya ba, domin tace, "wanda ya aikata ta, tag are ta ne zai rayu."*

**Amsa Wandannan Tambayoyi:**

- Mun zo wurin Almasihu domin muna bin doka ne? ___________________________________
- Za mu iya bin dokar Allah da kan mu? ____________________________________________
- Doka ya ce za mu iya yin wani abu na kanmu (ayyuka masu kyau) domin mu samu ceto da rain a har abada.  Wannan gaskiya ne? ____________________________________________

  Me ake nufi da "rayuwa na har abada" ko rain a har abada? _________________________

  ______________________________________________________________________________
- Bisa ga wannan wuri, za mu iya zaman kubuta da Allah ta wurin ____________________

<u>**Karanta Galatiyawa 4:4-7 (Alheri da Ceto)**</u>

*"Amma da lokaci ya yi sosai, sai Allah ya aiko Dansa, haifaffen mace, haifaffe kuma a karkashin shari'a, domin ya fanso wadanda suke a karkashin shari'a, mai da mu a matsayin ya'yan Allah. Tun da yake ku ya'yan ne, sai Allah ya aiko da Ruhun Dansa a cikin zukatanmu, yana kira, ya Abba! Don haka, kai ba bawa ba ne kuma, amma da ne. Da yake da ne kuma, to magaji ne bisa ga ikon Allah." Allah zai ba ka abin da ya alkawarta domin kai da ni.*

**Amsa Wadannan tambayoyi:**

- Wanene ya sayi yancinmu daga zunubi? ______________________
- Masu bada gaskiya ya'yan wane ne yanzu? ______________________

**<u>Karanta Galatiyawa 5:16-18; 24-25 (Alheri da Ruhu Mai Tsarki):</u>**

*"Maganata ita ce, ku yi zaman Ruhu, ba kuwa za ku biye wa halin mutuntaka ba. Don halin mutuntaka gāba yake yi da Ruhu, Ruhu kuma yana gāba da halin mutuntaka. Wadannan biyu gāba suke yi da juna, har ba kwa iya yin abin da kuke so. In Ruhu ne yake bi da ku, ashe, shari'a ba ta da iko da ku, ke nan.*

*"Wadanda kuwa suke su na Almasihu Yesu ne, sun giciye halin mutuntaka da mugayen sha'awace-sha'awace iri iri. In dai rayuwar tamu ta Ruhu ce, to, sai mu tafiyar da al'amuran mu ta wurin ikon Ruhu."*

**<u>Amsa Wadannan Tambayoyi</u>**

- Idan mu ma biyan Almasihu Yesu ne, to, menene muka giciye? ______________________
- Ta wurin wanene muka sami sabuwar rayuwa, wanene zamu bi acikin sabon rayuwarmu? ______________________

  ______________________

**<u>Read Galatians 6:14 (Grace and the Glory):</u>**

*"I hope I will never brag about things like that. The cross of our Lord Jesus Christ is my only reason for bragging. Through the cross of Jesus my world was crucified and I died to the world."*

**<u>Karanta Galatiyawa 1:5 (Alheri da Dauka)</u>**

*"Daukaka ta tabbata a gare shi har abada abadin. Amin"*


**<u>Amsa Wadanan Tambayoyi</u>**

- Ko zan iya yin fahariya da wani abinda na yi domin ceton kaina? ______________________
- Zan daukaka wanene a rayuwa ta? ______________________

**Abin yi 1: Hoton Alheri Tsantsa/Activity**

Umarnai:

- Yi amfani da wannan hoto domin ya taimake ka gane Alheri Tsantsa da yadda za ka bayyana ma wadansu.
- Cika wuraren da ba rubutu kana amfani da hoto na shafi 7 domin ya taimake ka.
- Ka iya bayyana hoton wa mai bi da kai?
- Rubuta sunan wani aboki a kasa da abin yi wanda za ka bayyana masa Alheri Tsantsa.




## Abin yi 2: Alheri Tsantsa. Cika inda ba Rubutu/Sa launi

<u>Umarnai:</u>

- Karanta kowane tambaya na kasa. Amsa kowane tambaya a inda babu rubutu.
- Ka yi launin hotunan.

## <u>Alheri Tsantsa. Cika inda ba Rubutu</u>

**Dokoki Goma**




Idan ka yi biyaya da dokoki 10 din, wanan ya isa ya yafe zunuban ka?

______________________________________

______________________________________

Me ya sa, Ko me yah ana?

______________________________________


______________________________________



Idan ba mu so mu zama bayin zunubi, wane ne kadai zai iya ba mu yanci?

______________________________________

______________________________________



Ina abubuwa masu kyau da Ruhu Mai Tsarki ke bayar idan mun bi Almasihu?

______________________________________

______________________________________


# V. TABBATATUN ALMAJIRAI CIKIN DAWAMAMMEN SHIRIN ALLAH

## Nazari 9

## Muna cikin Dawwamammen Shirin Allah domin Masu Binsa

[Tabbatattun Almajirai cikin Dawamammen Shirin Allah]

## Iyalin Allah




**Allah ya zabi wadanda suna binsa domin su zama cikin madawwammen shirin Allah, wanda shi ne Ikkilisiyarsa da Almasihu kamar kan sa.** Allah ya albarkace mu da sabon matsayi cikinsa da dukiya na ban mamaki kamar masu binsa ya nuna mana tawurin Maganarsa yadda ya kamata mu yi da rayu.

**<u>Ayoyin Hadacewa</u>**
**Afisawa 1:22-23**
*"Allah kuma ya sarayar da kome a karkashin ikon Almasihu, ya kuma ba da shi ga Ikkilisiya ya zama kai mai mallakar abu duka. Ikkilisiya ita ce jikin Almasihu cikar mai cika dukkan abu."*

**<u>Karanta Afisawa 1:7-10, 19-23 (Shirin Allah madawwami)</u>**
*"Wanda muna da fansarmu a cikinsa ta wurin jininsa, gafarar laifofinmu, gwargwadon wadatar alherinsa, wanda ya yawaita shi zuwa gare mu cikin dukan hikima da kaifin hankali, da ya sanar mana da asirin nufinsa, bisa ga yardansa da ya nufa a cikinsa zuwa wakilci na cikar wokatai, shi tattara dukan abu cikin Kristi, abubuwan da ke cikin sammai da abubuwan da ke bisa duniya; a cikinsa, na ke cewa."*

*"Da ko menene mafificin girman ikonsa zuwa gare mu, mu masu-bada gaskiya, gwargwadon aikin nan na karfin ikonsa wanda ya aikata cikin Kristi, sa'anda ya tashe shi daga cikin matattu, ya zamshe shi a hannun damansa cikin sammai, gaba nesa da dukan sarauta, da hukunci, da iko, da mulki, da kowane suna wanda ake ambatonsa, ba cikin wannan zamani kadai ba, amma cikin zamani mai-zuwa kuma: ya sarayar da dukan abu kuma karkashin sawayensa, ya sanya shi kuma shi zama kai a bisa abu duka ga Ikkilisiya."*

**Amsa Wadannan Tambayoyi:**

- Saboda jinin Almasihu da alherin Allah, mun zama ________________________ da yan ta da mu ________________________________________________ daga zunubanmu.
- Shirin Allah shi ne kowane abu cikin Sama da duniya za a hada shi tare cikin ________ __________________________ da ____________________ kamar kai.
- Wane Kungiya ne jikin Almasihu? ______________________________________________
- Wa zai iya hada jikin Almasihu masu bada gaskiya da ake kira Ikkilisiyarsa? __________ ______________________________________________________________________

**<u>Karanta Afisawa 1:3-14 (Albarku da Dukiya cikin Shirin Almasihu).</u>**

*"Albarka ga Allah da Uba na Ubangijinmu Yesu Kristi, wanda ya albarkace mu da kowace albarkan ruhaniya cikin sammai cikin Kristi: kamar yadda ya zabe mu a cikinsa tun kafin kafawar duniya, domin mu kasance masu-tsarki marasa-aibi a gabansa cikin kauna: bayan da ya rigaya ya kadara mu da zaman 'ya'yansa ta wurin Yesu Kristi, bisa ga yardan nufinsa, zuwa yabon darajar alherinsa, wanda ya kyautas mana a lokacin da ya mai da mu karbabbu cikin kaunatacen: wanda muna da fansarmu a cikinsa ta wurin jininsa, gafarar laifofinmu, gwargwadon wadatar alherinsa, wanda ya yawaita shi zuwa gare mu cikin dukan hikima da kaifin hankali, da ya sanar mana da asirin nufinsa, bisa ga yardansa da ya nufa a cikinsa zuwa wakilci na cikar wokatai, shi tattara dukan abu cikin Kristi, abubuwan da ke cikin sammai da abubuwan da ke bisa duniya; a cikinsa, na ke cewa. A cikin shi muna da gado saboda ya rigaya ya kadara mu gwargwadon niyyansa: shi wanda ke aikata dukan kome ta wurin shawararsa kadai domin mu kasance ga yabon daukakarsa, mu wadanda mun rigaya mun kafa begenmu ga Kristi. A cikinsa kuma, da kuka ji maganar gaskiya, bisharar cetonku, a cikinsa, sa'anda kuka bada gaskiya kuma, aka hatimce ku da Ruhu Mai-Tsarki na alkawari.*

**Amsa Wadannan Tambayoyi**

- Cikin Almasihu, Allay ya ba masu binsa dukan ____________________________________
- Sake duba da shugabanka albarku da dukiyoyi [dubi Rubutu a bisa] da mu ke da su a Dawwamamiyar Shirin Allah. Rubuta uku daga cikinsu a inda ba rubutun. ___________ ______________________________________________________________________ ______________________________________________________________________

**Karanta Afisawa 2:1-16 (Sabon Matsayi Cikin Shiring Almasihu)**

*"Ku kuma ya rayar da ku, yayinda ku ke matattu ta wurin laifofinku da zunubanku, inda kuke tafiya a da bisa ga zamanin wannan duniya, karkashin sarkin ikon sararin sama, ruhun da ke aiki yanzu a cikin 'ya'yan kangara; a cikinsu kuwa mu duka muna zamanmu a da a cikin sha'awoyin jikinmu, muna bin gurin jiki da na tnani; bisa ga tabi'a kuma 'yan tawaye ne, kamar sauran mutane: amma Allah, domin mawadaci ne cikin jinkai, saboda kaunarsa mai-yawa wanda ya kaunace mu da ita, ko lokacin da mu ke matattu ta wurin laifofinmu, ya rayar da mu tare da Kristi (ta wurin alheri an cece ku), ya tashe mu tare da shi, ya zamshe mu tare da shi cikin sammai, cikin Kristi Yesu. Domin cikin zamanu masu-zuwa shi bayyana mafificiyar wadatar alherinsa cikin nasiha zuwa gare mu cikin Kristi Yesu, gama bisa ga alheri an cece ku ta wurin bangaskiya; wannan kuwa ba daga gare ku ba ne, kyauta c eta allah: ba daga ayyuka ba ne, kada kowane mutun shi yi fahariya. Gama Shi ya kera mu halittattu muke cikin Kristi Yesu zuwa kyawawan ayyuka don mu yi tafiya a cikinsu. Domin wannan fa ku tuna, ku da Al'ummai na cikin jiki ne, wadanda a ke kira Marasa-kaciya tab akin wanda ana ce da ita kaciya (abin da hannu ke yi cikin jiki); a loton nan a ware kuke daga Kristi, rababbu daga taruwar Israila, baki ga wa'adodin alkawari, marasa bege marasa Allah cikin duniya. Amma yanzu cikin Kristi Yesu ku da kuke manisanta a da, cikin jinin Kristi an maishe ku kusa. Gama shi ne salamarmu, wanda ya maida mutane kasha biyu nan daya, ya kuma rushe bango mai-rabawa da ke tsakani, bayan da ya kawar da magabtaka cikin jikinsa, wato shari'a ta dokoki na cikin farillai; domin daga cikin biyu din nan shi halici mutum daya sabo cikin kansa, da haka nan a yi salama; cikin jiki daya shi sulhunta su biyu ga Allah ta wurin giciyen, bayan da ya kasha magabtaka ta wurinsa."*

**Amsa Wadannan Tambayoyi**

- Da mu matattu ne cikin zunuban kafin mu bi Almasihu. Mene ne sabon matsayin mu yanzu? ____________________
- Wata rana idan mun mutu za mu zama da wurin zama a ina da wane ne? ____________________

**Karanta Afisawa 3:16-19 (Addu'a domin Madawwamin Shirin Almasihu):**

*"Shi yarda maku, bisa ga wadatar darajarsa, a karfafa ku da iko ta wurin Ruhunsa cikin mutum na ciki; Kristi kuma shi zamna cikin zukatanku ta wurin bangaskiya; domin ku, dasassu ne kafaffu kuma cikin kauna, ku karfafa da za ku ruska, tare da dukan tsarkaka, k menene fadin da raar da tsawon da zurfin kaunar Kristi. Ku sani kuma kaunar Kristi, ku sani kuma kaunar Kristi wanda ta wuce gaban a san ta, domin ku cika har zuwa dukan cikar Allah."*

**Amsa Wadannan Tambayoyi**

- Ina wadansu abubuwa da Bulus ya yi addu'a Allah ya ba wadanda sun bada gaskiya a gareshi? ______________________________
______________________________
______________________________
______________________________

**Abin yi 1: Halaye da ya dace da Membobi cikin madawwamiyar Shirin Allah**

Umurnai:

- Karanta kowane shafi a kasa. Sake duba lissafin halaye na membobi cikin madawamamiyar shirin Allah a kasa.
- Hada halin da ya dace da shafi da ya bayyana shi.
- Rubuta halin da ya dace a kowane wurin da ba rubutu.

**HALAYEN MEMBOBI CIKIN MADAWWAMAMIYAN SHIRIN ALLAH**

Afisawa sura 4, 5 da 6 ya fada akan yadda masu bada gaskiya Kirista za su yi da kuma rayuwa cikin madawwamamiyan shirin Allah da kuma manufa. Wadansu halayen su ne:

**Tsarki** **Haske** **KaunaHadin kaiDaidaituwa** **Nasara** **Lura**

- **Tafiya cikin______________________________(Afisawa 4:16)**
  *"Domin ta gare shi ne dukkan jiki yake a game, yake kuma a hade, ta wurin gudunmawar kowace gaba, ta wurin kuma aikin kowace gaba daidai jikin yake kara girma, yana kuma ingantuwa da halin kauna."*

- **Tafiya cikin________________________(Afisawa 4:22-24)**
  *"Ku yar da kalinku na dā wanda dā kuke a ciki, wanda yake lalacewa saboda sha awoyinsa na yaudara, ku kuma sabunta ra'ayin hankalinku, ku dauka sabon halin nan da aka halitta bisa ga kamannin Allah da hakikanin adalci da tsarki."*

- **Tafiya cikin________________________(Afisawa 5:1-2)**
  *"Saboda haka sai ku zama masu koyi da Allah, in ku kaunatattun ya'yansa ne. Ku yi zaman kauna kamar yadda Almasihu ya kaunace mu, ya kuma ba da kansa dominmu, sadaka mai kanshi, hadaya kuma ga Allah."*

- **Tafiya cikin_________________________(Afisawa 5:8-11)**
  *"domin dā ku duhu ne, amma a yanzu ku haske ne a cikin Ubangiji. Ku yi zaman mutanen haske, domin haske shi ne yake haifar duk abin da yake nagari, na adalci da na gaskiya. Ku dai tabbata abin zai gamshi Ubangiji. Ku yi nesa da ayyukan duhu na banza da wofi, sai dai ku tona shu."*

- **Tafiya cikin___________________________(Afisawa 5:15-17)**
  *"Saboda haka, sai ku mai da hankali kwarai ga zamanku, kada ku zama kamar marasa hikima, sai dai masu hikima. Ku yi matukar amfani da lokaci don kwanaki mugaye ne. Don haka kada ku zama marasa azanci, sai dai ku fahimci abin da ya na nufin Ubangiji."*

- **Tafiya cikin____________________________(Afisawa 5:33; 6:1-2)**
  *"Duk da haka dai, sai kowane dayanku ya kaunaci matarsa kamar kansa, ita matar kuma ta yi wa mijinta ladabi. Ku ya'ya, ku yi wa iyayenku biyayya tsakani da Ubangiji, domin wannan shi ne daidai. Wannan shi ne umurnin farko mai alkawari, cewa, "ka girmama mahaifinka da mahaifiyarka."*

- **Tafiya cikin ___________________________(Afisawa 6:10-13)**
  *"A karshe kuma, ku karfafa ga Ubangiji, ga karfin ikonsa. Ku yi damara da dukan makamai na Allah, don ku iya dagewa gaba da kissoshin Iblis. Ai, famarmu ba ta yan adam muke yi ba, amma da mugayen ruhohi ne na sararin sama, masarauta, masu iko, da wadan da ragamar mulkin zamanin nan mai duhu take hannunsu.*
  *Saboda haka, sai ku dauki dukan makamai na Allah, domin ku iya dagewa a muguwar ranar nan, bayan kuma kun gama kome duka, ku dage."*

## Abin yi 2: Cika inda ba rubutu- Madawwamamiyar Shirin Albarku na Allah

Umurnai:

- Karanta ayoyi na hotunan. Cika kalmomi da ba su a ciki a inda ba rubutu.
- Ka yi launin hotunan.

## Dawamamiyar Shirin Albarku na Allah







Albarku biyu daga Allah cikin Afisawa 1:7

Sune _______________ da _______________

An ambata albarka daya har sau 6

cikin Afisawa 3:14-21. Shi ne: _________



Albarku biyu da an yi ta ambata a kai a kai cikin Afisawa 3:18-19 da 5:8-10.

Sune ________________________________ da ________________________________

**Abin yi 3: Makaman Allah**

**Umarnai:**

- Makaman Allah cikin Afisawa 6:11-18 albarka ne domin ya taimake mu yaki da mugun. Yana gutsure 7. Karanta Afisawa 6:11-18.
- Ka sa lamba na gutsure na makamin a inda ya yi dai dai a hoton sojan.





1. Gaskiya ta zama damararku
2. Adalci ta zama sulkenku
3. Bishara ta zama maker takalmi
4. Garkuwar Bangaskiya
5. Kwalkwahin ceto

6 da 7. Takobin Ruhu (Maganar Allah) da Addu'a cikin Ruhu koyaushe.

# VI. TABBATATUN ALMAJIRAI CIKIN GIDAN ALLAH

## Nazari 10
## Masu Bada Gaskiya suna cikin Gidan Allah
### [Tabbatatun Almajirai cikin Gidan Allah]
## Iyalin Allah




**Ikkilisiya, Gidan Allah ya hada dukan masu bada gaskiya da masu bin Yesu Almasihu, su yi aiki dai dai.** Bulus yana so ya tabbata matashin nan abokinsa Timoti, ya gane yadda za a sarrafa Ikkilisiya na farko muhimmancin koyaswa sahihiya, zaman tsarki da wadatan zuci, zaben shugabanai na ruhaniya, da zaman iyali dai dai.
Koyarwan Bulus suna mana da muhimmanci a Gidan Allah yau. Yayin da mun koya, dole mu mika ma wadansu ta wurin horad da su da kuma almajirantad da su.

**<u>Ayar Hadacewa:</u>**

**I Timoti 4:12**
***"Kada ka yarda kowa ya raina kurciyarka, sai dai ka zama gurbi ga masu ba da gaskiya ta wurin Magana, da hali, da kauna, da bangaskiya da kuma tsarkaka."***

**Karanta I Timoti 3: 14-15**

*"Ina sa zuciya in zo a wurinka ba da dadewa ba, amma ina rubuto maka wadannan abubuwa, don in ya acena yi jinkiri za ka san irin zaman da ya kamata a yi a jama'ar Allah, wadda take tace Ikkilisiyar Allah Rayayye, jigon gaskiya da kuma ginshikinta."*

**Karanta I Timoti 2:4-6**

*"Wanda yake son dukkan mutane su sami ceto, su kuma kai ga sanin gaskiya. Domin Allah daya ne, matsakanci kuma daya ne, a tsakanin Allah da mutane, Almasihu Yesu, mutum, wanda ya ba da kansa fansa saboda kowa da kowa: An kuma yi shedar wannan a dai dai lokacin sa."*

**Amsa Wadannan Tambayoyi**

- Bulus ya ce iyalin Allah shi ne ____________________
  (Ana kuma kiranta Gidan Allah)
- Wane ne Allah yana so ya samu ceto? ____________________
- Bulus yana da ganewa sosai akan yadda mutane za su iyawa samun ceto (domin su hadu da iyali ko Gidan Allah). Hanya daya ne kadai. Mene ne shi? ____________________

  ____________________

**Karanta I Timoti 1:9 (Gina akan kwakwaran koyaswa daga Maganar Allah)**

*"Kana rike da bangaskiya da lamiri mai kyau. Gama wadansu mutane saboda kin kasa kunne ga lamirinsu, suka lalatar da bangaskiyarsu."*

**Karanta I Timoti 2:1-3 (Addu'a)**

*"Da farko dai ina gargadi, cewa a yi ta rokon Allah, ana addu'a, ana gode wa Allah saboda dukkan mutane da sarakuna da kuma duk wadanda suke a manyan makamai, don mu zauna lafiya, rai a kwance, muna bin Allah sosai a cikin natsuwa. Wannan kyakkyawan abune, kuma abin karba ne a gun Allah Mai Cetonmu."*

**Amsa Wadannan Tambayoyi:**

- Mene ne shawaran Bulus ga Timoti? ____________________
- Mene ne hatsarin rashin bin shawaran Bulus? ____________________
- Bulus ya ce Timoti, da fari yana da muhimmanci a yi? ____________________
- Za ka iya yin lissafin wadanda Bulus ya ce Timoti ya yi masu addu'a?
  - ____________________
  - ____________________
  - ____________________
  - ____________________

**Karanta I Timoti 4:1-16 (Horo domin cikin Gidan Allah)**

*"Amma Ruhu yana fadi a sarari, cikin kwanaki na karshe wadansu za su ridda daga imani, suna maida hankali ga ruhohi na rudani da koyarwar aljanu, ta wurin riyar mutane masu-fadin karya, wadanda an yi ma lamirinsu lalas sai ka ce da karfe mai-wuta, suna hana yin aure, suna hukunta a bar cin abinci iri iri, abin da Allah ya halitta domin a karbe shi da godiya ke nan a wajen masu-bada gaskiya masanan gaskiya. Gama kowace halittar Allah mai-kyau ce, ba kuma abin da za a ki idan da godiya aka karbe shi ba ne: gama ya tsarkaka ta wurin maganar Allah da addu'a.*

*Idan ka tuna ma 'yan'uwa wadannan abu, ka zama nagarin mai hidima na Kristi Yesu, kiyayayye cikin zantattukan imani, da na koyarwar kirki wanda ka bi har wa yau: amma tatsuniyoyi na sabo da irin na gyatumai sai ka ki su. Ka wasa kanka zuwa ibada: gama wasa jiki tana da anfaninta kadan: Amma ibada tana da anfani ga dukan abu, da ya ke tana da alkawari ga rai na yanzu, da na mai-zuwa. Batun nan mai-aminci ne, ya kuwa isa kowa ya karba. Zuwa wannan fa muke wahala muna kuwa kokari, domin muna da begenmu a kafe ga Allah mai-rai, shi da shi ke Mai-ceton dukan mutane, tun ba wadanda ke bada gaskiya. Wadannan abu sai ka umurta, ka koyas kuma.*

*Kada kowa ya rena kuruciyarka: amma ka zama gurbi ga masu-bada gaskiya, cikin Magana, tasarrufi, kauna, bangaskiya, da tsabtar rai. Ka maida hankali ga karatu da gargadi da koyarwa, har na zo. Kada ka yi banza da baikon da ke cikinka, wanda aka ba ka bisa ga annabci, tare da dibiyawar hannuwa na jama'ar firesbita. Ka yi kwazo cikin wadannan al'amura: ka bada kanka gare su sosai; domin cingabanka ya bayanu ga kowa. Ka maida hankali da kanka, da kuma koyarwarka. Ka lizima cikin wadannan: gama garin yin wannan za ka ceci kanka duk da masu-jinka."*

**Amsa Wadannan Tambayoyi:**

- Rubuta abubuwa uku da Bulus ya ce **a yi** a wannan wurin: ____________________________
  ____________________________________________________________________________________
  ____________________________________________________________________________________
- Rubuta abubuwa uku da Bulus ya ce **kada a yi** ________________________________________
  ____________________________________________________________________________________
  ____________________________________________________________________________________
- Domin kana matashi, har yanzu kana da muhimmanci cikin iyali ko a Gidan Allah? ____
  ____________________________________________________________________________________
- A cikin I Timoti 4:7-8, Bulus ya ce, "hori kanka ga __________________________." Ya ce horon "_____________________________________ yana da amfani ta kowace hanya."
- Domin kana da muhimmanci, Allah yana son ka zama__________________________ ta hanyar rayuwa ta Almasihu domin wadan su (I Timoti 4:12).

**<u>Karanta I Timoti 5:1-3, 8:</u>**

*"Kada ka tsauta wa dattijo, sai dai ka roke shi kamar mahaifinka. Sanan kuma ka dauke shi kamar 'yan'uwanka, tsofaffi mata kuma kamar uwayenka, 'yan mata kuwa kamar 'yan'uwanka, da matukar tsarkaka.*

*Ka grimama gwamraye mata, wadanda ba sa da mataimaka.*

*Duk wanda bai kula da danginsa ba, tun ba ma iyalinsa ba, ya mŭsa wa bangaskiya ke nan, ya kuma fi marar ba da gaskiya mugunta."*

**<u>Karanta I Timoti 6:8-10:</u>**

*"To, in muna da abinci da sutura, ai, sai mu dangana da su.*
*Masu dokin yin arziki kuwa, sukan zarme da jaraba, su fāda a cikin tarko, suna mugayen sha'awace-sha'awe iri iri na wauta da cutarwa, irin wadan da suke dulmuyar da mutane, su kai ga lalacewa da hallaka."*

*Ai, son kudi shi ne tushen kowane irin mugun abu. Don tsananin jarabar kudi kuwa wadansu mutane, har sun baude wa bangaskiya, sun jawo wa kan su bakin ciki iri iri masu sukar rai."*

<u>Amsa Wadannan Tambayoyi</u>

- I Timoti 5:1-2, ya ce koyaushe mu daukaka mutane kashi hudu "a hanya tsantsa."

| **Kungiyan** | **Daukaka** |
|---|---|
| Tsofoffi maza | Kamar____________________________ |
| Samari | Kamar____________________________ |
| Tsofoffi mata | Kamar____________________________ |
| Yan mata | Kamar____________________________ |

- Wane ne zai lura da gwamraye wadanda su kadai ne? ________________________________
- Wane ne zai lura da dangi na masu ba da gaskiya? __________________________________
- <u>Kaunar</u> kudi yana da kyau/mugu. Wanne ne dai dai? _________________________________
- I Timoti 6:8-10 ya ce mana kada mu doki son arziki domin mu ji dadi amma mu ______________________________________________ da abin da muke da shi.

**Karanta Afisawa 5:22-25 (Tsarin Iyali a Gidan Allah)**

*"Ku matan aure, ku yi biyayya ga mazanku, Ubangiji ke nan kuke yi wa.*
*Don miji shi ne shugaban matarsa, kamar yadda Almasihu yake shugaban Ikkilisiya, wato jikinsa, shi kansa kuma shi ne Mai Ceton Jikin.*

*Kamar yadda Ikkilisiya take bin Almasihu, haka kuma mata su bi mazansu ta kowane hali.*
*Ku maza, ku kaunaci matanku kamar yadda Almasihu ya kaunaci Ikkilisiya, har ya ba da kansa dominta."*

**Karanta Afisawa 6:4**

*"Ku ubanni, ka da ku sa 'ya'yanku su ji fushi, sai dai ku goye su da tarbiyya, da kuma gargadi ta hanyar Ubangijinku."*

**Karanta Titus 2:4**

*"Ta haka su koya wa mata masu kuruciya su so mazansu da ya'yansu."*

**Karanta Kolosiyawa 3:20-21**

*"Ku ya'ya, ku yi wa iyayenku biyayya ta kowane hali, domin haka Ubangiji yake so.*
*Ku ubanni, kada ku kuntata wa 'ya'yanku, domin kada su karai."*

**Amsa Wadannan Tambayoyi**

- Wane ne kan Ikkilisiya? ______________________________
- Wa ya kamata ya zama kan iyali? ______________________________
- Yaya ya kamata maza su kaunaci matansu? ______________________________
- Yaya ya kamata iyaye za su da ya'yansu? ______________________________
- Yaya ya kamata ya'ya za su da iyayensu? ______________________________

**Abin yi: Hoto/Launi**

Ka yi launin wanna hoto

# Bulus da Timoti



**Abin yi 2: Ginin Gidan Allah**


Umarni:

- An kira Bulus gwanin magini cikin I Korantiyawa 3:10. Yana so "gina" Gidan na Allah (Ikkilisiyar Allah) da taimakon membobi su yi karfi cikin Ubangiji.
- Wa'azi da rubuce rubucen wasikunsa sun zama kamar kayan da magini zai yi amfani da shi domin "gina" masu ba da gaskiya cikin Gida na Allah.
- Domin kowane wasika na Sabon Alkawari (kayan gini) da an nuna a kasa, rubuta manufa da sun yi dai dai yadda Bulus yana so ya cim ma buri cikin wasikarsa. [Ka iya yin amfani da zane na nazari t 8-10 domin ya taimake ka.

**Hada wadannan manufofin wasikun Bulus a kasa**

- **Wasika na farko <u>koyaswan Bisharan Alheri Tsantsa</u>.**
- **Wasika na tsakiya <u>koyaswan Manufa da Shirin Allah.</u>**
- **Wasika na karshe <u>koyaswan Tsari Dai Dai na Gidan Allah.</u>**

## Ginin Gida na Allah

| | | |
|---|---|---|
|  |  |  |
| **Littafi: <u>Galatiyawa</u>**<br>**Manufa**<br>________________<br>________________<br>________________<br>________________ | **Littafi: <u>Afisawa</u>**<br>**Manufa**<br>________________<br>________________<br>________________<br>________________ | **Littafi: <u>1 Timoti</u>**<br>**Manufa**<br>________________<br>________________<br>________________<br>________________ |

**Abin you 3: Tsarin Iyali cikin Gida na Allah**

Umarnai:

- **Ka sake karanta Afisawa 5:22-24; Afisawa 6:4; Titus 2:4; Kolosiyawa 3:20-21 da I Timoti 5:1-3.** Wadannan wurare suna Magana akan tsari mai kyu na iyali cikin Gida na Allah bisa ga Littafi Mai Tsarki. **Allah ya zana Gidansa domin ya kasance da tsari na shugabanci da ban girma.** Kamar misali, za mu girmama wadanda Allah ya sa su cikin shugabanci a bisanmu, kamar iyayenmu ko masu lura da mu da shugabannan Ikkilisiya.
- Kewayen Tsari na **Iyali cikin Gida na Allah** abin yi da na biye zai iya taimakon ka fahimtar inda ka ke cikin Gida na Allah.
- **Cika inda ba rubutu da launin kewaye na kasa. Tattauna abin yi da kungiyarka ko kowane shugaba.**


1. Giciye na tsakiya manadin Almasihu ne. Wane ne ya kamata ya kasance a tsakiyar ran kowane **daya** da iyali? Kamar matashi, da ko diya wanda mai ba da gaskiya ne cikin Yesu Almasihu, kana cikin tsakiya da Almasihu. Rubuta sunanka a karamin kawanya a tsakiya da giciyen. Yi launin kowane kawanya da **Rawaya**. **Dangantakarka da Yesu Almasihu yana da muhimmanci domin sani da biyaya ga Almasihu zai taimake ka zaman memban iyali nagari cikin iyali da na Ikkilisiya.**

2. Kawanya na biyu na tsakiya manadin **aure** tsakanin mutum daya (miji) da mace daya (mata). Rubuta sunaye mama da babank cikin kawanyan idan ba ka san sunayensu duka ba kaiya rubuta sunan daya da ka sani, ko ka bar wurin ba rubutu. Yi launin kawanyan auren da **shudi**.

3. Kawanya na uku daga tsakiya manadin **iyali** ne. Wannan kawanya ya hada da iyaye kuma cikin wannan kawanyan da sunayen yan'uwa maza da mata. Iyali ba duka iri daya ba. Maimakon iyaye suna zama da kai, kila kana da su kaka ne, ko yan'uwa manya ko manya masu lura da kai. Ka iya rubuta suna/sunaye na **wandanna mutanen cikin wannan kawanyan ma.** Yi launin iyalin da kore.

4. Kawanya na hudu daga tsakiya manadin **Ikkilisiya, Gida na Allah.** Kawanyan ya kumshi dukkan masu bada gaskiya koina a duniya, hade da tsofofi maza, mata. Matasa masu ba da gaskiya ga Yesu Almasihu za su kasance cikin wannan kawanya ma. Rubuta sunan mai bada gaskiya daya da ka sani wanda ya grime ka ko sunan masujadan ka. Yi launin kawanyan masujadan da **algashir.**

# Tsarin Iyali Cikin Gidan Allah




# VII. TABBATATUN ALMAJIRAI CIKI DA TARE DA ALMASIHU

## Nazarin 11

## Rayuwa Cikin Almasihu Yesu




**Allah yana ba masu binsa arziki cikin Almasihu, tawurin bangaskiya cikin Dansa, na ban mamaki fiye da ganewarmu da zai dawama har abada!** Ba ceto kadai mu ke da shi ba amma da rai na har abada, amma kuma muna da salama, sabon rai, kurkusa da Allah, da sauran albarku masu yawa.

**Ayan Hadacewa:**

**Filibiyawa 4:19**
*"Allahna kuma zai biya muku kowace bukatarku daga cikin yalwar daukakarsa da take ga Almasihu."*

**Karanta Matiyu 13:44 – 46**

*"Mulkin sama kamar dukiya yake da take binne a gona, wadda wani ya samu, ya sake binnewa, yana tsaka da murna tasa, sai ya je ya sayar da dukan mallaka tasa, ya sayi gonar.*
*Har wa yau kuma mulkin sama kamar atajiri yake mai neman lu'ulu'ai masu daraja. Daya sami lu'ulu'ai mai tamanin gaske, sai ya je ya sai da dukan mallaka tasa, ya saye shi."*

**Amsa Wadannan Tambayoyi:**

- Matiyu ya kwatanta mulkin sama da abubuwa biyu masu daraja. Mene ne su?

  ______________________________, ______________________________

- A abin yi a kasa, ka ja layi daga aya/ayoyi da sun yi dai dai "dukiya cikin Almasihu" a yadda ayan ya bayyana.

| **Ayoyi** | **Dukiya Cikin Almasihu** |
|---|---|
| Afisawa 1:5 | Kauna |
| 1:7 | Bege da Hakuri |
| 1:13 | Cikake da Rai na Gaskiya |
| 1:9 | Gafarar Zunubai |
| 2:5 | Salama |
| 2:6 | Sabon Rai |
| 2:7 | Ceto |
| 2:13 | Baban Iko/Karfi Cikin Ruhaniya |
| 2:14 | Sama |
| 3:19 | Kurkusa da Allah |
| Kolosiyawa 2:9-10 | Alheri |
| 2 Tasalonikawa 2:16-17 | Zama Ya'yan Allah |

- Kolosiyawa 2:9-10 ya ce, *"Domin a cikinsa ne cikin jiki dukkan cikar Allahntaka take tabbata. A gare shi ne aka kammala ku, wanda yake shi ne shugaban dukkan sarauta da iko."* Menene a ke nufi da Almasihu a cikin ka? ______________________________

  ______________________________________________________________________

  ______________________________________________________________________

- 2 Tasalonikawa 2:16, ya ce, *"To, Ubangijinmu Yesu Almasihu kansa, da kuma Allah Ubanmu, wanda ya kaunace mu, ya kuma ba mu madawwamiyar ta'aziya da kyakkyawan bege ta wurin alherinsa."* Menene Ubangijinmu Yesu Kristi da Allah Uba sun ba mu? ______________________________________________________

  ______________________________________________________________________


  ______________________________________________________________________

**Abin yi 1: Zana Akwatin Baitulmalin**

<u>Umarni:</u>

- Ka zana akwatin baitulmalin, ka bi lambobin akwatin.

# Zana Akwatin Baitulmalin




**Abin yi 2:"Cikin Almasihu" Zanen hannu**

<u>Umarnai:</u>

- Giciyen yana nuna Yesu Almasihu. Idan ka amince Almasihu ya yafe zunubanka, ka zama sabon halitta "cikin Almasihu" tare da albarku masu yawa. Idan ka amince da Yesu kuma yanzu kai memba na iyalin da Jigin Almasihu, ka cika hoto na kasa domin ya nuna sabon matsayinka.
- Da yatsanka na farko akan kurtun tawada da Mai bi da kai zai tanada, sa ka danna yatsan cikin giciyen.

[Misali  ]

## Zannen Hannu "Cikin Kristi"s



# Nazari 12

# Rayuwan <u>Tare</u> da Almasihu



Wata babban gatanci da mai ba da gaskiya yana da shine tafiyarsa a gaba Allah rayaye. **Daukan lokaci tare da Allah kowace rana yana da babban muhimmanci a rayuwar ka na ruhaniya da tafiya <u>tare</u> da <u>Almasihu</u>.** Kuma abu mai kyau shi ne **Allah yana so mu dauki lokaci da yin zumunci tare da shi.** I Korantiyawa 1:9 ya ce, *"Allah mai alkawari ne, shi kuma ya kira ku ga tarayya da Dansa Yesu Almasihu Ubangijinmu."* Rayuwa tare da **Almasihu yana nufin abokantaka tare da shi.** Idan ka dauki lokaci kai kadai da Ubangiji, kana ma'amala da wanda ya fi duka.

**<u>Ayan Hadacewa</u>**
**Wahayin Yahaya 3:20**
*"Ga ni nan a tsaye a bakin kofa, ina kwankwasawa, kowa ya ji muryata ya bude kofar, sai in shiga wurinsa, in ci abinci tare da shi shi kuma tare da ni."*

**<u>Karanta Luka 24:13–32</u>**

*"Ga kuma guda biyu daga cikinsu suna tafiya a ran nan za su wani kauye wanda ake ce da shi Immawus, nisansa daga Urushalima mil bakwai ne da rabi. Suna zance da junansu a kan*

*dukan al'amuran nan da suka faru. Ananan suna cikin zance suna bincike tare da juna sai Yesu da kansa ya kusance su, ya tafi tare da su. Amma idanunsu a kame su ke da ba za su sansance shi ba. Ya kuwa ce masu, Wane irin zance ke nan ku ke yi da juna, kuna cikin tafiya, da fuskoki a kwantsare? Dayansu wanda ake ce da shi Kilyobas, ya amsa ya ce masa, Kai kadai kake bako cikin Urushalima, ba ka san al'amuran da suka faru a nan cikin wadannan kwanaki ba? Ya ce masu, wadanne al'amura? Suka ce masa, A kan zancen Yesu Ba-nazarat, wanda shi ke annabi mai-iko cikin aiki duk da Magana a gaban Allah da dukan jama'a: manyan malamai kuma da mahukumtanmu suka bashes hi ga hukumcin mutuwa, suka giciye shi kuma. Amma mu da muna sa bege shi ne zai shi fanshi Isra'ila. Bayan wannan kuma yau rana ta uku ce da wadannan abubuwa suka faru. Kuma wadansu mata daga cikin jama'armu, da suka tafi wurin kabarin tun da sassafe suka rude mu; gama sa'anda ba su iske jikinsa ba, suka zo, suka ce sun ga ru'ya kuma na mala'iku, wadanda suka ce yana da rai. Wadansu daga cikin wadanda ke tare da mu kuma suka rafi wurin kabarin, suka iske hakanan ne kamar yadda mattan suka fadi amma shi kansa ba su ganshi ba. Ya ce masu, Ku mazaje marasa-wayo, masu-nauyin zuciya ga gaskantawa dukan abin da annabawa suka fadi! Ba wajib ne ga Kristi ba shi sha wadannan wahalai, shi shiga cikin darajassa kuma? Ya soma tun daga Musa da dukan annabawa, cikin dukan litattafai yana fassara masu al'amura na bisa kansa.*

*Suka kusato kauyen da za su: shi ma ya yi kamar za ya wuce. Suka matsa masa, suka ce, Ka zauna tare da mu: gama maraice ta kusa, yini kuwa ya kusa karewa. Ya kuwa shiga garin shi zauna tare da su garin ci, sai ya dauki dunkulen gurasa, ya albarkace shi, ya kakkarya, ya ba su.*

**<u>Amsa Wadannan Tambayoyin</u>**

- Me ya sa Kiliyobas da abokinsa na bakin ciki da suna tafiya a hanya zuwa Imuwasu?

  ____________________________________________________________
- Wane ne bako da ke tafiya tare da mutum biyun? ____________________________
- Mene ne bakon ya ce wa mutum biyu din akan wannan ranar? ____________________

  ____________________________________________________________
- Yaushe suka gane tabbatace ko wane ne wannan bakon? ________________________

  ____________________________________________________________

**<u>Karanta Galatiyawa 5:16:</u>**

*"Maganata ita ce, ku yi zaman Ruhu, ba kuwa za ku biye wa halin mutuntaka ba."*

Idan mun rayu tawurin bin Ruhu wanda yanzu yana cikin mu, ba zamu sake;

______________________________ zama na Shaitan

______________________________ son bin hanyar zunubi

______________________________ sauran abin da Allah yana so daga gare

**Karanta Kolosiyawa 2:6:**

*"Da yake kun yi na'am da Almasihu Yesu Ubangiji, to, sai ku tsaya a gare shi."*

| Bayan mun yi na'am da Almasihu, wanda a ciki muke rayuwa (mu na wane ne?) |
|---|
| ____________________ Shaidan |
| ____________________ Kanmu |
| ____________________ Almasihu |

**Karanta Romawa 6:4:**

*"Saboda haka, an binne mu da shi ke nan, ta wurin baftisma cikin mutunwarsa, domin yadda aka ta da Almasihu daga matattu ta wurin daukakar Uba, haka mu ma mu yi zaman sabuwar rayuwa."*

| Wane irin rayuwa Allah yana so mu yi cikin Almasihu? |
|---|
| ____________________ iri na kafin mu san Almasihu |
| ____________________ Sabon rai cikin Almasihu |
| ____________________ son zuciya na yin abin da na ke so |

**Karanta afisawa 5:2:**

*"Ku yi zaman kauna kamar yadda Almasihu ya kaunace mu, ya kuma ba da kansa dominmu, sadaka mai kanshi, hadaya kuma ga Allah."*

| Wannan Sabon Rai cikin Almasihu zai ba mu zaben mu yi rayuwa na |
|---|
| ____________________ kauna |
| ____________________ tsoro |
| ____________________ shakka |

**Karanta Joshua 1:8:**

*"Kada wannan littafin dokoki ya rabu da bakinka, amma zai zamo abin da za ka yi ta tunani a kansa dare da rana domin ka kiyaye, ka kuma aikata bisa ga dukan abinda aka rubuta a ciki, gama ta haka za ka yi albarka cikin hanyarka, ta haka kuma za ka yi nasara."*

| Sau nawa za mu yi tunani akan maganar Allah? |
|---|
| ____________________ lokacinda muna so |
| ____________________ wani lokaci |
| ____________________ kowane lokaci (dare da rana) |

**Karanta Matiyu 6:33:**

*"Muhimmin abu na farko, sai ku kwallafa rai ga al'amuran mulkin Allah da kuma adalcinsa, har ma za a kara muku dukan wandannan abubuwa."*

| Me masu ba da gaskiya za su fi so a rayuwa? |
|---|
| ________________________________ mulkin Allah |
| ________________________________ abin da Allah ke so |
| ________________________________ samu abu mai kyau da farinciki |

**Karanta Yahaya 15:4–6, 10:**

*"Ku zauna a cikina, ni kuma a cikinku kamar yadda reshen inabi, ba ya iya 'ya'ya shi kadai, sai ko ya zauna itacen inabin, haka ku ma ba za ku iya ba, sai kun zauna a cikina. Ni ne itacen inabin, ku kuma rassan. Wanda ya zauna a ciki na, ni kuma a cikin sa, shi ne mai yin ya'ya da yawa. Domin in ba game da ni ba, ba za ku iya kome ba. Duk wanda bai zauna a cikin, za a yar da shi can, kamar reshe, ya bushe, a kuma tattara irinsu a jefa wuta, a kone.*

*In kun bi umarnina, za ku zauna cikin kaunar da nake muku, kamar yadda ni na bi umarnin Ubana, na kuma zauna cikin kaunar da yake mini."*

| Me ake nufi da "Ku Zauna" cikin Almasihu? |
|---|
| ________________________________ yi abin da na tuna yana da kyau? |
| ________________________________ biyayya da umarnin Allah |
| ________________________________ zauna cikin kaunar Almasihu |

**Abin yi 1: Hoto/Yin Launi**

Za ka iya launin wannan shafin

# <u>Yesu a Hanya Zuwa Imuwasu</u>



**Abin yi 2: Rayuwarka Tare da Almasihu. Warkan Abin yi**

Umarnai:

- Allah yana so mu zama da dangantaka na kusa da shi.
  Karanta ayoyin na kowane hoto a kasa. Domin kowane tsari, rubuta kuma ka yi magana akan yadda ayoyin/hoto ya nuna abin da Allah ke nufi, Ubanmu na sama.
- Ka iya gama hanyoyin sai ka yi launin hotunan

# Rayuwarka Tare da Almasihu


1. **Karanta Luka 15:1-7 – Batacciyar Tunkiya**



2. **Karanta Luka 15:8-10 - Bataccen Kudi**



3. **Karanta Luka 11:11-32 - Da da Ya Bar Gida**



4. **Karanta Yahya 15:4-10- Itacen Inabi da Ratsanta**



# Nazari 13

# Lokaci da Ubangiji kowace Rana



**Kasance da Ubangiji kowace rana, samun lokaci da Ubangiji,** ba abin yi mai kyau kadai ba. Yana da muhimmanci da albarka, cikake, da rayuwar murna cikin Almasihu. Kamar yadda muka koya a Nazari 12, muna bukata mu zo kusa da Almasihu. Zama abokaninsa (I Korantiyawa 1:9). Muna yin wannan tawurin samun tabbatacen lokaci tare da shi.

__Ayoyin Hadacewa__
**Zabura 119:9-11**
"Kaka saurayi za I kiyaye ransa da tsarki? Sai ta wurin biyayya da umarnaka. Da zuciya daya nake kokarin bauta maka, Ka kiyaye ni daga rashin biyayya da umarnanka! Na rike maganarka a zuciyata, don kada in yi maka zunubi."

**__Menene__ Lokacin Shiru?**

- Kasance da Lokacin Shiri. Shine samun lokaci kowace rana domin karatu da nazarin maganar Allah cikin Littafi Mai Tsarki da yin addu'a zuwa gareshi.

**__Karanta Yakubu 4:8[a]:__**
*"Ku kusance Allah, shi ma zai kusance ku."*

**__Karanta Afisawa 6:18:__**
*"A koyaushe kuna addu'a da roko ta wurin ikon Ruhu ba fasawa. A kan wannan manufa ku tsaya da karfinku da matukar naci, kuna yi wa dukan tsarkaka addu'a."*

**__Karanta Irmiya 29:12:__**
*"Sa'an anan za ku yi kira a gare ni, ku yi addu'a a wurina, zan kuwa ji ku."*

**<u>Karanta Kolosiyawa 4:2:</u>**

*"Ku lazamci yin addu'a, kuna zaune a fakade a kanta sosai, tare da gode wa Allah."*

**<u>Karanta Zabura 1:2-3:</u>**

[Mutum mai farincike ne idan] *"Maimakon haka, yana jin dadin karanta shari'ar Allah, yana ta nazarinta dare da rana. Yana kuma da itacen da yake a gefen korama, yakan ba da ya'ya a kan kari, Ganyayensa ba sa yin yaushi, yakan yi nasara a dukan abind da yake yi."*

**WadanAmsa nan Tambayoyi:**

- Yakubu 4:8 gayyata garemu domin mu zo ________________________________ idan mun yi haka, me Allah zai yi ______________________________________________
- Zabura 1 ya ce, yana da kyau mu kaunace koyaswan Ubangiji cikin Littafi Mai Tsarki da tunani akan abin da ya koyawa mana yaushe? ____________________________
- Ta yaya za mu zo kusa da Allah da koyo akan koyaswansa kowace rana? ___________ ____________________________________________________________

## <u>Me ya sa</u> muna bukatar Lokaci da Ubangiji?

**<u>Karanta Joshua 1:8:</u>**

*"Kada wannan littafin dokoki ya rabu da bakinka, amma zai zama abin da za ka yi ta tunani a kansa dare da rana domin ka kiyaye, ka kuma aikata bisa ga dukan abinda da aka rubuta a ciki, gama ta haka za ka yi albarka cikin hanyarka, ta haka kuma za ka yi nasara."*

**<u>Karanta Yahaya 15:14-15:</u>**

*"Ku aminaina ne in kuna yin abinda na umarce ku. Nan gaba ba sauran in ce da ku bayi, don bawa bai san abind da Ubangijinsa yake yi ba. Sai dai in ce, da ku duk abin da na jiyo wurin Ubana."*

**<u>Karanta Luka 6:12:</u>**

*"A kwanakin nan Yesu ya fita ya hau dutse domin yin addu'a. Dare karai yana addu'a ga Allah."*

**<u>Amsa Wadannan Tambayoyi:</u>**

- Musa ya ce wa Joshua (Joshua 1:8) ya yi abubuwa uku da Littafi Mai Tsarki. Mene ne wadannan abu uku? __________________, ____________________, ________________
  Wannan shi ne abind da Allah yana so muma mu yi.
- A Yahaya 15:14, idan muna so a kira mu "abokane" na Almasihu, dole mu yi abin da shi ______________________________________________________________
  Samun Lokaci kadai hanya ne da Allah zai sa mu san abin da shi yana so mu sani da abin da za mu yi.

- A kalla sau shida Littafi Mai Tsarki ya yi Magana akan Yesu ya tafi wani wuri shi kadai domin ya yi addu'a. Idan Yesu yana bukata kasance shi kadai tare da Ubansa cikin sama, shi kuma Allah ne, ko muna bukata mu kasance da Allah kowace rana? Don me? Me ya sa ba bukata? (Tattauna da yara) ____________________________________________
____________________________________________
____________________________________________
- Me ya sa Yesu zai bukaci a dauki lokaci tare da Ubansa na sama? ____________________
____________________________________________

**Karanta Matiyu 4:4:**

*"Amman Yesu ya amsa ya ce, "A rubuce yake cewa, 'Ba da gurasa kadai mutum zai rayu ba, sai dai da kowace maganar da ya ke fitowa daga wurin Allah."*

**Bitrus I Bitrus 2:2:**

*"Kamar jariri sabon haihuwa, ku yi marmarin shan madara marar gami mai ruhu, domin ku girma da shi, har ya kai ku ga samun ceto."*

**Amsa Wadannan Tambayoyi**

- Mun sani muna bukatar abinci domin mu rayu. Yesu ya ce muna bukatar wani abu fiye da abinci domin mu rayu a hanya daidai. Muna bukata mu rayu ____________________
____________________________________________
- Tawurin koyo daga Littafi Mai Tsarki tsansan. Koyaswa mai sauki, ya taimake ka yin me? ____________________________________________
____________________________________________

## Yaushe ya kamata mu samu lokaci a kadaice?

**Karanta Matiyu 6:11:**

*"Ka ba mu abincinmu na yau"*

**Karanta Zabura 5:3:**

*"A gare ka zan yi addu'a, ya Ubangiji, Da safe zan ka ji muryata. Da hantsi zan yi addu'ata, in kuma jira amsa."*

**Karanta Markus 1:35:**

*"Da assusuba ya ta shi ya fita, ya tafi wani wuri inda ba kowa, ya yi addu'a a can."*

**Karanta Matiyu 14:23:**

*"Bayan ya salami taron, ya hau dutse shi kadai domin ya yi addu'a har magariba ta yi yana can shi kadai."*

**<u>Amsa Wadannan Tambayoyi</u>**

- Muna cin abinci na jiki kowace rana. Muna kuma bukatar abinci na ruhaniya, Gurasan Rai da maganar Allah, domin rayuwa a hanyar da ya yi dai dai. Sau nawa ya kamata za mu "ci" (nazarin maganar Allah da addu'a) abincin ruhaniya? ______________________
  ________________________________________________________________________________
- Sarki Dauda, cikin Tsohon Alkawari, yana son Magana da Allah da safe. Mun sani cewa wadansu lokaci Yesu yakan yi Magana da Ubansa da safe da kuma magariba wadansu lokaci. Akwai damuwa akan kowane lokaci na kasance kadai? ____________ Abin da ya fi muhimmanci shi ne? ________________________________________________________
  ________________________________________________________________________________

## <u>A ina</u> za mu kasance a lokacin kadaici?

**<u>Karanta Matiyu 6:6:</u>**

*"Amma in za ka yi addu'a, sai ka shiga lollokinka, ka rufe kofa, ka yi addu'a ga Ubanku wanda yake boye, Uban ku kuwa da yake ganin abin da ake yi asirce, zai sāka maka."*

**Karanta Luka 5:16:**

*"Amma shi, sai ya rika kebanta a wuraren da ba kowa, yana addu'a"*

**<u>Karanta Wadannan Tambayoyi</u>**

- Yi tunani a inda kake yanzu. Inda akwai tsit, wuri a kadaice inda za ka iya samun lokaci a kadaice? ____________________________________________________________
  ________________________________________________________________________________


# <u>Ta yaya</u> za mu iya samu lokaci a kadaice?

- Je a Abin yi 3: Shirin Lokaci a Kadaice a karshen Nazari 13 domin amsar wannan tambaya.

**Abin yi 1: Hoto/Launi**

Za ka iya yin launin hoton

# <u>Yesu Yana Addu'a Cikin Jeji</u>



**Ayoyin Hadacewa: Zabura 119:9-19**

*"Kanda saurayi zai kiyaye ransa da tsarki? Sai ta wurin biyayya da umarnanka. Da zuciya daya nake kokarin bauta maka, ka kiyaye ni, daga rashin biyayya da umarnanka! Na rike maganarka a zuciyata, don kada in ji maka zunubi."*

**Abin yi 2:Me Nake Bukata Domin Lokacin na Kadaita?**

Umarnai:
A kasa ga lissafin wadansu abubuwa da an saba karanta kowane lokaci.

- Idan ka yi tunani abin yana da taimako kuma yana da kyau ka kasance da shi lokacin kadaicinka, sai ka sa alama ¤ a gefen abin.
- Idan ka yi tunani abin da kyau ka kasance da shi lokacin kadaicinka, sai ka **X** a gefen abin

---

Littafi Mai Tsarkin ka ________________________

Biskit /Kek ________________________

Fensir/alkalami/mujalla ________________________

Takardan rubutu/takarda ________________________

Abin wasan yara ________________________

Na'uran wasani/waya ________________________

Lissafin bukatun Addua'ta ________________________

Kanina/Yar'uwata ________________________

Jagoran Nazarin Littafi Mai Tsarki ________________________

## Ka iya bayyana amsoshinka

________________________________________________________________

________________________________________________________________

________________________________________________________________

________________________________________________________________

________________________________________________________________

________________________________________________________________

________________________________________________________________

**Abin yi 3:Shirin Lokacin Kadaita**

Umarnai:

- Karanta shirin Lokacin Kadaita a hankali. Wata ra'ayi ne guda daya na yadda za ka fara Lokacin Kadaita tare da Almasihu.
- Ba Ka'idaden akan kowane sashe. Dole ka yi shawara abin da ya yi maka dai dai: Za ka iya yin canji yadda ake bukata.

# Shirin Lokacin Kadaita

**Addu'ar budewa** ------------------ Roki Allah ya albarkaci Lokacin Kadaitar ka da kuma Ruhu Mai Tsarki ya taimake ka gane abin da ka ke so ka koya.

**Karatun Littafi Mai Tsarki** ------ Karanta wurare na musam-man na Littafi Mai Tsarki bisa ga shirin kamar shiri na kwana 31 na Gamuwa da Yesu cikin Darasi ta 14.

**Nazarin Littafi Mai Tsarki** ------ Yi amfani da Matakai Hudu na Hanyar Nazarin Littafi Mai Tsarki cikin darasi ta 6 da 7 domin ya taimake ka gane da yin aiki da abin da ka karanta. Rubuta abin da ka koya cikin majalla na kullum. Rubuta tambayoyi da har yanzu kana da su.

**Lokacin addu'a** ------------------- Yi Magana da Allah a kai a kai. Yi addu'a domin bukatun ka da na wadansu. Yana jin ka kuma yana so ka zo wurinsa. Kada ka manta ka yabe shi da yi masa godiya domin dukan abin da ya yi. [Abin yi da Lissafin Addu'a Na Kanka a Darasi ta 14 zai kara bi da kai da kana Magana da Allah].


**Samo taimako** -------------------- Yi tunani akan kowane tambayoyi da kana da su akan abin da ka karanta. Roki Ruhu Mai Tsarki ya nuna maka ma'anar sa. Idan har yanzu kana da tambayoyi, ka iya zaba ka yi amfani da Jagoran Nazarin Littafi Mai Tsarki ko sharhi domin kara samun bayyani ko tambayi babban mutum da ka amince da shi domin ya taimake ka.

**TUNA**

- Tsaya akan tafarkin. Tsaya kan fasalinka na kullum
- Sake, duban abin da ka koya akai a kai
- Nemi taimako lokacinda kana bukata domin ka gane abin da ka yi nazarinta.
- Yi addu'a domin hikima da fahimtar abin da ka karanta kogyo
- Yi canji a rayuwanka in Allah ya sa ka yi haka.
- Idan wani rana ya wuce ka, kada ka karaya.

# Nazari 14

## Taimako Domin Addu'a da Sujada



**Lokacinda mun yi addu'a da sujada, muna sadarwa kai tsaye da wannan Allah da halitta dukkan ababe.** Ce ka iya magana da Allah kai tsaye, kana masa godiya, yabonsa, da rokonsa. Yana sha'awa mu yi haka! yana so mu yi zumunta na kusa da shi Babanmu na cikin Sama. Darasi ta 13 ya yi magana akan muhimmancin Samun Lokaci a kadaice kowace rana. Wanda ya hada da nazarin Littafi Mai Tsarki da addu'a. Wannan darasi yana kara Magana akan addua'a da sujada, wadanda sashe ne na Lokaci a Kadaice, amma zai iya faru a kowane lokaci.

__Ayan Hadacewa__
**Zabura 7:17**
*"Zan gode wa Ubangiji saboda adalcinsa, zan raira yabbai ga Ubangiji, madaukaki."*

__**Karanta I Tassalonikawa 5:17:**__
*"Ku rika yin addu'a ba fasawa."*

__**Karanta Filibiyawa 4:6:**__
*"Kada ku damu da kome, sai dai a kowace hali ku sanar da Allah bukatunku ta wurin yin addu'a da roko, tare da gode wa Allah."*

__**Amsa Wadannan Tambayoyi**__

- Wani lokaci ya dace da yin addu'a? (__Zabi amsa daya daga kasa, Kewaye shi__).
  Sau daya a wata/ Sau daya a kowane rana/ Kowane lokaci.

- Me za mu iya magana akai da Allah? (__zabi amsa daya a kasa. Kewaye shi__).
  Kowane abu/ Abin da nake so ya bani/ Sai abin da ya dame ni kadai

Wani lokaci muna bukatar taimakon sanin yadda za mu yi addu'a. Ga jerin abu hudu domin addua da zai taimake yin addu'a da ya fi kyau.

| | |
|---|---|
| **A.** | **GIRMAMA – Tunani akan iko, alfarma, da daukaka na Allah.**<br>*"Yabo, da girma, da daukaka, da mulki sun tabbata ga wanda yake a zaune a kan Kursiyin, da Dan Ragon nan, har abada abadin!"* Wahayin Yahaya 5:13[b] |
| **C.** | **FURTA LAIF** – **Gaya wa Allah kasawarka domin zunubi da ka yi yanzu.**<br>*"In kuwa muka bayyana zunubanmu, to, shi mai alkawari ne… zai kuwa gafarta mana zunubanmu."* (I Yahaya 1:9[a]) |
| **T.** | **GODIYA- Gode ma Allah domin dukkan abin da ya yi da abinda da ya ke yi kowane rana.**<br>*"Mu zo gabansa da godiya, mu raira wakokin farinciki na yabo!"* (Zabura 95:2) |
| **S.** | **ROKO - Roki Allah saboda ababa da kana bukata ko wandansu mutane za su bukata**<br>*"kada ku damu da kome, sai dai a kowanne hali ku sanar da Allah bukatunku, ta wurin yin addu'a da roko, tare da gode wa Allah."* (Filibiyawa 4:6). |

<u>**Amsa Wadannan Tambayoyi**</u>

- Cika ayoyin Littafi Mai Tsarkin nan akan yabo da sujadar Allah a kasa. Dubi ayoyin. Rubuta hanyoyi dabam dabam na yabo da sujadan Allah da na cikin ayoyin.

## <u>Ayoyin Littafi Mai Tsarki akan yabo da Sujada ga Allah</u>

**Karanta kowane aya a kasa. Rubuta hanyoyi da za mu iya yabo da sujada ga Allah**

Zabura 95:6 - ______________________________

Zabura 46:10 - ______________________________

Ibraniyawa 13:15 - ______________________________

Zabura 14:9-13 - ______________________________

Zabura 95:1 - ______________________________

Zabura 150:4 - ______________________________

Zabura 47:1 - ______________________________

Yahaya 13:34-35 - ______________________________

Nehemiya 8:6 - ______________________________

Hanyoyin yabo da sujada ga Allah kashi nawa ka samu? ______________

Ka iya tuna wadansu hanyoyi na yabo da sujada ga Allah? ______________

______________________________

**Abin yi 1: Hoto/Launi**

Ka Yi Launin Wannan Hoto

## Yara Na Addu’a



Yara Na Sujada



**Ayan Hadacewa**

**Zabura 7:17**

*“Zang gode wa Ubangiji saboda adalcinsa, zan raira yabbai ga Ubangiji, Madaukaki”*

**Abin yi 2: Lissafin Rokon Addu’a na Kanka/Hannun Addu’a**

Umarnai:
- Ka yi amfani da lissafin Rokon Addu’a na Kanka domin ya taimake ka cikin addu’a.

## Lissafin Rokon Addu’a na Kana

1. Iyali/Abokanai (Iyaye, membobi wadansu iyali, mutane na kusa da kai etc). ______________________________
2. Iyali na Ikkilisiya/Mishan (Fasto, Malamai, Mishanari, etc). ______________________________
3. Manyan Gwamnati (Shugabanai kamar President, Gwamna, Sarki, Alkalai, Wakilai etc). ______________________________
4. Mutane marasa lafiya ko masu bukata (a jiki ko damuwar ruhaniya) ______________________________
5. Ni da kaina (girma a ruhaniya, hikima, lafiyar jiki, makaranta, aiki etc.) ______________________________

**Hanun Addu’a**
- Ka iya yin amfani da wannan hanun addu’a domin ya taimake ka tuna yin addua domin ya taimake ka tuna yin addu’a na kanka.
- Kowace yasa na tsaye wa rukuni ta yi addu'a daga na sirin bukatun addu'a



**Abin yi 3:Taimako Domin Lokacin Kadaita Cikin Maganar**

Umarnai:

- Sake duba matakai na nazarin Littafi Mai Tsarki Darasi na 6 da 7.
- Gwada yin amfani da matakan domin ka yi nazari wata sashe daga Littafi Mai Tsarki.

# Taimakawa Mai Amfani don Lokacin shuru a cikin kalma

Taimako Domin Lokacin Kadaita cikin Maganar Domin ya taimaka fara cikin maganar kowace rana, ka koma baya da sake duba Darasi ta 6 da 7 akan yadda za ka yi Nazarin Littafin Mai Tsarki. Kuma, dauki dan takarda ko takardan rubutu sai ka rubuta cikin matakai uku a kasa domin ka rubuta inda ka kai cikin Littafi Mai Tsarki. Misali, dauki Zabura 23:1-9 sai ka bi wadannan matakan. Za ka bukata Karin layi a cikin takardan rubutunka fiye da layi na kasa. Da shi ke wannan shi ne nazari na Lokacin Kadaita na kanka, ba za ka kara matakai na Tattaunwa (daga Darasi na 6 da 7). Ka iya tattauna tunaninka da wadansu daga baya. Ka tuna ka yi addu'a da ka fara Lokacin Kadai na ka.

**1. LURA- "DUBA SHI" – Me yana cewa?** ______________________________

______________________________

______________________________

______________________________

______________________________

**2. TUNANI- "YI TUNANI A KAI" – Me ya ke nufi?** ______________________________

______________________________

______________________________

______________________________

______________________________

**3. AIKATAWA- "ZAUNA A CIKI" – Yi shi yanzu fa?** ______________________________

______________________________

______________________________

______________________________

______________________________

**Ka lura**

Domin Nazarin Littafi Mai Tsarki na tsawan wata, ka iya amfani da karatu da Nazarin Littafi Mai Tsarki na gamuwa da **Yesu na kwana 31** da aka shirya a wannan darasi. Ka iya dauka kowane kan magana da sashen Littafi sai ka yi amfani da hanyar nazari na bisa sashen. Bayan **kwana 31 na gamuwa da Yesu,** ka iya fara karatun dukkan Littafi Mai Tsarki ko wasiku bisa ga bishewar Ruhu Mai Tsarki. Akwai Karin taimako na karatun Littafin Mai Tsarki domin ya taimake ka a karshen Darasi na 14, **a shirin karatu na Shekara Guda.**

**Abin yi 4: Kwana 31 Na Gamuwa da Yesu**

Umarnai:

- Ka iya bin wannan shirin Karatun Littafin Mai Tsarki na wata Guda domin ya taimake ka a lokacin shirin kadaitawa domin ka karu da sanin Yesu, Maganar Rai.

# Kwana 31 Na Gamuwa da Yesu

| Rana | Kan Magana | Littafi |
|---|---|---|
| Rana 1 | Anabci akan Yesu | Ishaya 53 |
| Rana 2 | Haifuwar Yesu | Matiyu 1:18-25 |
| Rana 3 | Yahaya Mai Baftisma ya shirya hanya | Matiyu 2:1-4: 11 |
| Rana 4 | Yesu da wata Basamariya | Yahaya 4:1-26 |
| Rana 5 | An ki Yesu a Gida Nazarat | Luka 4:14-30 |
| Rana 6 | Yesu ya kira Almajiransa | Luka 5:1-11 |
| Rana 7 | Wa'azi wani sarari | Luka 6:17-46 |
| Rana 8 | Yaran Gwamruwa da Mace Mai Zunubi | Luka 7:11-17; 7:36-50 |
| Rana 9 | Yesu ya Gamu da Farisiyawa | Matiyu 12:1-13, 22-45 |
| Rana 10 | Misali da Mai Shuka | Matiyu 12:1-43 |
| Rana 11 | Yesu ya tsawata wa Hadiri | Luka 8:22-25 |
| Rana 12 | Warkar da Mai Aljan da Yar Yayirus | Markus 5:1-43 |
| Rana 13 | Yesu ya ciyad da Mutum 5,000 | Yahaya 6:1-14 |
| Rana 14 | Bitrus ya San Almasihu | Luka 9:18-27 |
| Rana 15 | Warkarwa ta Bangaskiya | Markus 9:14-32 |
| Rana 16 | Karin Koyaswa da Misalai | Matiyu 17:24-18:20 |
| Rana 17 | Karin Koyaswa da Misalai | Matiyu 18:21-19:15 |
| Rana 18 | Saurayi Mai Dukiya | Markus 10:17-31 |
| Rana 19 | An aiki Almajirai | Luka 10:1-24 |
| Rana 20 | Umarni mafi Girma | Markus 12:28-44 |
| Rana 21 | Misalin Basamariya Mai Jinkai | Luka 10:25-37 |
| Rana 22 | Addu'ar Ubangiji | Luka 11:1-13 |
| Rana 23 | Yesu ya Tada Li'azaru daga Mutuwa | Yahaya 11:1-44 |
| Rana 24 | Shigan Urushalima cikin Nasara | Matiyu 21:1-27 |
| Rana 25 | Jibin Ubangiji | Yahaya 13:1-17 |
| Rana 26 | Kaunar Yesu ga Almajiran | Yahaya 14:15 |
| Rana 27 | Kama Yesu da Basheshi | Matiyu 26:36-75 |
| Rana 28 | Shari'ar rashin adalci akan Yesu | Yahaya 18:19-19:16 |
| Rana 29 | Giciye da Mutuwar Yesu | Yahaya 19:17-42 |
| Rana 30 | Tashin Yesu da Bayyanuwa | Yahaya 20-21 |
| Rana 31 | Babban Umarni na Yesu | Matiyu 28:16-20 |

## Karin Hanyoyi na Nazarin Maganar Allah a Shafi Biyu Gaba

## Shirin karatun Littafin Mai Tsarki cikin shekara


Ka tuna, in ka karanta cikin Maganar Allah, wanda ita ce Gaskiya. Gaskiya mutum ne, Yesu Almasihu, Maganar Allah Mai Rai kuma dukkan Maganar Allah na nuna gareshi ne. Lura wannan abin yi yana cikin Lokacinka na Kadaitawa. Ka iya raba aikin kowane mako domin ka karanta duka cikin kwana 7, ba za ka tattauna karatun da wadansu a lokacin karatun ba, daga baya ka iya fada abin da ka koya tawurin nazari maganar da kanka.

# TSARIN KARATUN LITTAFI MAI TSARKI

| MAKO | KAN MAGANA | LITTAFI | KARATU |
|---|---|---|---|
| 1 | Allah ya Halitce Adamu & Hawawu | Farawa 1-2:24 | |
| 2 | Maciji | Farawa 3 | |
| 3 | Labarin Nuhu | Farawa 6:9-9:17 | |
| 4 | Labarin Abram | Farawa 15 | |
| 5 | Labarin Saraya | Farawa 18:1-15; 21:1-6 | |
| 6 | Labarin Yakubu | Farawa 27; 32-32 | |
| 7 | Labarin Yusufu | Farawa 37; 39-42; 44-45 | |
| 8 | Labarin Maryamu | Fitowa 2:1-10 | |
| 9 | Allah ya ceci Isra'ilawa | Fitowa 12:1-42; 14:5-31 | |
| 10 | Musa da Dokoki Goma | Fitowa 20:1-21 | |
| 11 | Labarin Haruna | Fitowa 32:1-29 | |
| 12 | Labarin Kalibu | Littafin Kidaya 13 | |
| 13 | Labarin Balaam | Littafin Kidaya 22:21-41 | |
| 14 | Labarin Rahab | Joshua 2 | |
| 15 | Labarin Joshua | Joshua 6 | |
| 16 | Labarin Deborah | Littafin Mahukunta 4 | |
| 17 | Labarin Gidiyon | Littafin Mahukunta 6-7 | |
| 18 | Rut da Na'omi | Rut 1-2 | |
| 19 | Labarin Hannatu | I Sama'ila 1:9-28 | |
| 20 | Labarin Sama'ila | I Sama'ila 16:1-3 | |
| 21 | Labarin Matashi Dawuda | I Sama'ila 17 | |
| 22 | Labarin Abigail | I Sama'ila 25:2-38 | |
| 23 | Labarin Sulemanu | I Sarakuna 3; Karin Magana 1:1-7; 2:1-22 | |
| 24 | Labarin Iliya | I Sarakuna 18:1-40 | |
| 25 | Labarin Elisha | 2 Sarakuna 4:1-7 | |

| MAKO | KAN MAGANA | LITTAFI | KARATU |
|---|---|---|---|
| 26 | Labarin Yosiya | 2 Sarakuna 22:1-23:25 | |
| 27 | Haikalin Allah | Ezra 3:1-13; 7:1-10; 9:6-10:17 | |
| 28 | Labarin Nehemiya | Nehemiya 3-4; 6 | |
| 29 | Labarin Esta | Esta 5:1-8; 8:1-17 | |
| 30 | Labarin Ayuba | Ayuba 1-2; 13, 40; 42 | |
| 31 | Maganar Sarki Dawuda | Zabura 23 | |
| 32 | Labarin Irmiya | Irmiya 1:3-19 | |
| 33 | Labarin Shadrak, Meshak da Abednego | Daniyel 3 | |
| 34 | Labarin Daniyel | Daniyel 6 | |
| 35 | Labarin Yunusa | Yunusa 1-4 | |
| 36 | Labarin Makiyaya | Luka 2:1-20 | |
| 37 | Labarin Maryamu | Matiyu 2:13-23 | |
| 38 | Labarin Yahaya Mai Baftisma | Yahaya 1:19-34 | |
| 39 | Labarin Nikodimu | Yohanna 3:1-2 | |
| 40 | Manzani | Matiyu 10 | |
| 41 | Labarin Saurayi Mai Arziki | Matiyu 19:16-30 | |
| 42 | Farisiyawa | Matiyu 22:34-40; 23:1-36 | |
| 43 | Labarin Maryamu da Marta | Yahaya 12:1-8 | |
| 44 | Babban Hadaya Na Yesu | Matiyu 27:27-28:10 | |
| 45 | Labarin Toma | Yahaya 20:24-30 | |
| 46 | Ikkilisiya ta Farko | Ayyukan Manzani 2 | |
| 47 | Labarin Bitrus | Ayyukan Manzani 3 | |
| 48 | Labarin Istifanus | Ayyukan Manzani 7 | |
| 49 | Labarin Filibus | Ayyukan Manzani 8:26-40 | |
| 50 | Labarin Shawulu | Ayyukan Manzani 9:1-19 | |
| 51 | Labarin Sila | Ayyukan Manzani 16:16-40 | |
| 52 | Labarin Timoti | Ayyukan Manzani 16:1-4;<br>1 Timoti 4:6-16; 6:11-21;<br>2 Timoti 1:3-14 | |
| **BONUS** | Yahaya ya Hangi Gaba | Wahayin Yahaya 21-22 | |

# Danka wa wadansu!



- Manufar wannan takardan nazari domin horad da **kai** ne a ka'idokin Littafi da Ikkilisiyar Farko ta yi aiki da shi da ya yadu da canja duniya ma Almasihu da Bishara a lokacin.

- Bukatarmu shi ne mu bunkasa sani da marmari da ke **cikinka**, kamar wanda yana yin wannan nazari, ka zama daya daga almajirai na yau da zai taba **duniyarka** domin Bishara.

- Muna fada maka abin da Bulus ya ce ma Timoti:

*"Abin da ka ji a guna a gaban shai'du masu yawa kuwa, sai ka danka wa amintattun mutane, wadanda su ma za su koya wa wadansu."*
**2 Timoti 2:2**

- Lokaci ya yi da **za ka danka wa wadansu** abin da ka koya akan zama memba na Iyalin Gidan Allah.

- Rubuta sunayen mutane biyu wadanda kana so ka danka masu abin da ka sani akan Iyalin Gidan Allah a fili na kasa.

__________________________________ __________________________________

- Fara yin addu'a domin zarafi na **danka wa wandasu**

# Satifikat Na Gamawa

## “Shirin Allah domin Almajirai Matasa”

Wannan Shaida ne cewa

________________________________________

Da nasara ya gama dukkan darisai da horaswa na Shirin Allah domin Almajirai Matasa

**Wannan ya hada da gabatarwa da nazari na kanka, tattaunawa, da abin yi a wadannan darisai goma sha hudu:**

1. Iko da Isan Maganar
2. Iko da Isan Ruhu
3. Baftisma ta Ruwa
4. Membobin Juna
5. Jibin Ubangiji

6/7. Umurnai a yadda za a ya Nazarin Littafi Mai Tsarki

8. Tabbatatun Almajirai Cikin Bishara ta Alheri Tsantsa
9. Tabbatatun Almajirai Cikin Shirin Allah na har Abada
10. Tabbatatun Almajirai Cikin Gidan Allah
11. Ran ka Cikin Almasihu
12. Ran ka Cikin Almasihu
13. Lokacin addu’a na Kowace rana tare da Ubangiji
14. Taimako Mai amfani domin Addu’a da Sujada

An mika wannan Satifikat wa dalibi a bisa daga New Foundation International da Sugaban Majami’a, da marmarin wannan dalibin ya yi girma kamar dalibi mai bada ya’ya domin daukakar Allah.

____________________ New Foundation International

____________________ Sugaban Majami’a

Yanzu danka ya zaba ya bi Almasihu yanzu sai me?
Ina huhimman ka'idodin na Littafi Mai Tsarki da suna bukata su sani domin su yi girmasu rika a almajirai na Yesu?

Koya wadannan ka'idodi ba lallai a yi da rikida ba, wadannan takardan almajiranci ba saishehunan ilimi za su koyadda shi. An shirya shi domin iyaye na joyar, malaman sande skulk o wadansu masu renonsu da almajirai ne. Kowane darasi an tanada jagora, domin mai koyaswan, Littafi Mai Tsarki, Ayoyin hadacewa, da hanaye na abin yi na yara.

Yara suna da muhimmanci a gaban Allah. Wannan gaskiya ne da Matiyu

> 18:10 ce: "Ku dai lura, kada ku raina daya daga cikin wadannan yan yara. Ina gaya muku,malaikunsu a sama kullum suna duban fuskar ubana da yake cikin sama".

Lokacin da yara sun zo wurin Almasihu da wuri za su yi rayuwarsu dukka domin sa, su yi girma kamar almajiransa da shaida wa wadansu. Wannan Littafin yana a yalwace kamarkayan aiki domin ya taimakesu su yi haka.
(Martha D. Evans, Director of Children Ministries, Fellowship Bible Church).



"Abin da ka ji a guna a gaban shaidu masu yawa kuwa, sai ka danka wa amintattunmutane, wadanda su ma za su koya wa wadansu." 2 Timoti 2:2

$12.95
ISBN 978-0-578-86396-2
51295>
9 780578 863962